abinda yagani ne ya bugar da zuciyarsa yayi saurin murxa idanunsa su din dai yagani manne da junansu ba wasu ba, har bunayya ya bud'e kofar bangaren ummi ,shine yasoma shiga can ya leko dakansa ya janyo hannunta suka shiga tare cikin minti biyu sai gashi ya sake fitowa ya nufi hanyar part dinsa .
Baba mai gadi ya dad'e tsaye yana mamakin abinda ya gani addua yayi musu ...

****

Washegari takama weekend da misalin karfe biyu na rana bayan sun gama cin abinci abi ya kira muwaddat ,ta taso daga inda take zaune ta zauna kasa agabansa ta lankwashe kafafunta ta kamo yatsun kafarsa tana matsa masa ahankali ahankali tana dubansa domin jin abinda zai fad'a.
"Murmushi yayi cike da jin dadi kana yace " na gode sosai diyata Allah yayi miki albarka.

a zahirin gaskiya duk ranar Dana aurar dake muwaddat zanyi kewa sosai ..
Tayi murmushin "InshaAllahu abi baza kayi kewar da zata haifar maka da damuwa ba, saboda duk Wanda zan aura zai kasance a kusa daku yake ,kullun adduarta Allah yabani miji kusa daku "
Abi yayi murmushi tare da cewa "ameen yanzu ma ai kinsamu murmushi kawai tayi tacigaba da matsa masa yatsun kafafunsa "da fari ina son muyi magana ta fahimtar juna dake akan lamarinki da bunayya " abinda nake so dake ki saida hankalinki guri daya ki daina biyewa shirmensa saboda har yanzu bunayya yaro ne k'arami akanki ko ba haka ba ?
Jikinta a matukar sanyaye tace "hake ne abi "

Abi ya numfasa yacigaba da mgn " ki maida hankali ki k'arasa karatunki ,karatunki na da matukar mahimmanci agareki dama al'umma gabadaya, domin ilimin diya mace na da matukar mahimmanci, idan kin gama karatunki ga suraj nan ya nuna alamun yana sonki da aure ..

Tayi saurin yatsina fuska ranta a 'bace tace "wani suraj kuma ?
"Waye ma suraj abi ? Tayi masa tambayar tana jin yadda zuciyarta ke bugu da karfi.
Yayi murmushi kawai sannan yace vice chairman na kamfanina mana.

"o oh to ni..ni abi bana son shi ,me zanyi dashi mummuna dashi .
abi yayi dariya "kai muwaddat manya ,ina ruwanki da muninsa halayye kirki ake bukata ba kyau ba, tayi murmushin "kawai abi ni bana sonshi gsky ,shikenan sai ki auri Umar kenan .
Ta zaro ido "wani Umar kuma ?
" dan makocina mana shima yana magun sonki har mahaifinsa yayi min magana "kai abi shima bana sonshi wallahi ,ya fiyye surutu dayawa bazan iya auren mai yawan magana ba "to shikenan sai ki auri nasir Dan abokina tunda naga shima yaron yana sonki "haba abi nasir din da mukayi karatu tare yamaza'a yi na auresa ,meye bambacinsa da bunayya da kace shirme yake sbd yace yana sona?

,"to to.. yanxu nagano bakin zaren kice kina son bunayya kenan ?
" saboda nasan shi ai ya had'a duka abubuwan da baki so ko?
Tayi murmushin "kai abi idan lokacin yayi zan zabo ma suruki kyakyawa mai hankali ,kuma mai wadataccen ilimi sannan Miskili dan ni banason nmj mai yawan magana nafi son shiru shiru cikin murmushi abi yace "ai duk wannan abubuwan da kika lisafin na bunayya ne sak kyakkawa miskili shiru shiru mara son mgn,,

tayi murmushi tana rufe idanunta" Allah abi ba hk bane "to shikenan Allah ya nuna mana lokaci da zarar kin kare karatu sai aure, saboda ina bukatar ganina da jikokina sukayi dariya gabadaya abi yace "kinga yanzu wannan zangon idan kun koma makaranta zaki kare karatunki ,kiyi kokari kafin lokacin ki samomin suruki, miskili kyakyawa shiru shiru na aura masa ke na huta suka sake kwashewa da wata dariya ....

suna cikin dariya bunayya ya d'aga labule yashigo parlour'n had'e da sallama yana gama shigowa parlour'n yace "hirar me akeyi haka ne ake kyalkyalewa da dariya ?
"nima gani nazo ayi dani, agaya dariyar me ake?

Abi yace "ina bata zabi ne cikin masu bugamana sammaci a gida " "haba abi meyasa kake irin haka ne ,byn kasan komai akaina?
cikin dry abi yace "o ni ishaq bunayya yaushe ka dawo haka ne ?

"To ni me nayi ?
ya fad'i hk yana take wa muwaddat kafa tare da sakar mata wani laulausar murmushi sharesa tayi saboda suna gaban abi ,ahankali ya rusuna da kwayar idanunsa mai nuna alamun tsokana yace "ta Alhaji nuhu kenan dama ni hakura nayi kawai ki karata da tsofafinki masu shegen muni ,dan ma kin samu yaro irina mai wankeken Jini yace zai aureki kikewa mutane salo gaki gasu alhj nuhu ..

"Dan Girman Allah ka rabani da zance mutumin nan yana 'bata min rai wallahi zan iya daina fita saboda shi ,"da kin kyauta min kuwa, ya fad'a hk da karyayye sauti mai nuna laushi ,ya sake russunar da kwayar idanunsa cikin nata ,suka lumshe atare sakamakon azababbiyar soysyyar da Allah yasanyawa zukatansu tun basu San me hakan yake nufi ba ..

Byn sun kammala abi ya Mike bunayya ya rufa masa baya zuwa bankony, suka zauna bisa irin sakakkun kujeru nan na gargajiya da'ake sakawa Wanda mafi akasari anfi samunsa a irin gidajen manya masu hannu da shuni..

Ganin haka yasa muwaddat ta nufi kitchen ta d'auko tire ta bud'e fridge ta d'auko ruwa da tattaciyar inibi kasancewar shi abi yafi so, ta nufo inda suke ta ajiye tayi gaba ,bunayya ya janyo jug din ya cikawa abi cup da ruwan inibi ya mikawa abi wannan ne kawai lemun da abi yafi so tun tasowarsa har bisa ga yanxu domin yana k'ara masa kuzari da mazantaka da wuya suyi

rashinsa acikin gidan, kafin yakare an kawo wani ,abi ya amsa yana yasoma sha yana kallon M. A yana murmushi domin yasan akwai magana abakinsa sai da M. A ya bari yagama sha sannan yace "abi ina son mu sake yin magana ta karshe da kai akan baby"uhmmm ina jinka fatan ka hakura ne kasoma neman admision na komawa karo karatu?
 "yanxu hk admission Dina na daf da fitowa daga jamiar Dana nema ,but nafi bukatar muwaddat arayuwata akan komai "abi ka daina ganin kankatata wallahi ko mata hud'u ka aura min zan iya rayuwa dasu ballanatana muwaddat da ban ta'ba jin wai yaya ce gare ni ba ...

Tunda yasoma magana abi yayi shiru yana nazarin maganarsa Anya ba hakura zaiyi ba kuwa Amman kuma ai mahaifiyarsa tace batason auren zumuncin , bugu da k'ari ina bunayya ina muwaddat?

A cewar ummi tayi masa girma kar azo a cutar daita daga baya azo ana danasani M.A ya numfasa yace "abi babu irin macen dake duniya nan da zata iya fin karfin nmj matukar ba lusari bane ,abi yayi murmushi yana dubansa ido cikin ido Amman ya kasa magana saboda alamarin M. A na neman fin karfinsa..
"shikenan zan sake tuntubar umminka "Dan Allah abi kashowo min kanta kaji ya k'arasa mgnr cike da shagwa'ba.

 "InshaAllahu zanyi iya kokarina, da wannan suka kawo karshen hirar tasu Wanda basu sani ba duk acikin kunne ummi sukayiwa koda abi ya sake tuntubarta da zance sharewa ummi tayi, tashiga wata tsabgar da hidimomin gabanta tare da bawa abi kulawa ganin take zance M. A shirme ne ,ta yaya za'a yi d'an 22 yres yayi aure?

****
 tana kwance a d'akinta taji motsi ana son shigowa d'akinta, zumbur ta Mike jikinta na rawa ta sauko daga Kan gadon tasoma lalu'ben makunnin wutan d'akin kafin ta kunna har ya karaso gareta ya rungumeta ajikinsa "ta bud'e bakinta zata kurma ihu yayi saurin rufe mata baki "baby ni ne fa "ta sauke naunayen ajiyar zuciya "na kasa bacci ne gashi na kira layinki yaki Shiga"dan Allah baby ki fito ki nunawa ummi kema kina sona mana , kuma ki zaki aureni ,ki nuna mata muna tsananin son juna ni dake, nasan zata fi fahimtarki akaina, dan nasan muddin taji komai daga bakinki zata yarda.

"wai dan Allah wa yace maka yana sonka ?
ni dai asanina ban ta'ba bud'e bakina nace ina sonka ba, kai ne dai ke shirmenka, kai ko ina sonka misali bazan iya furtawa ummi ina sonka ba, dana furta haka gara .. hk nan tayi shiru ta kasa k'arasa mgnrta.

"meyesa kike yi shiru?

"ki karasa maganarki mana, ba adduar mutuwa zakiyiwa kanki ba akan karya ba?

"kina sona muwaddah ,nasani kina sona so kuwa mai girma amman na rasa dalilin da yasa kike

nuna kmr baki sona, sannan kike nunawa ummi babu komai atsakaninmu alhali akwai .
"me yasa muwaddah?
ya k'arasa mgnr yana shafa mata sansar jiki.

"bunayya ka daina plz""kema ki daina abinda kike min ,ki daina boyewa ummi komai har dayasa take ganin rashin dacewarmu.....

numfasa tayi cikin sarkewar murya tace
"Ummi na gani rashin dacewar aurenmu da kai, kmr yadda ni kaina nake hange ,bunyya kai kani nane ...ahalin yanzu ma so nake nayi maka iyaka da komai nawa ..lips dinta ya kamo yasoma tsotsa har ya bud'e bakinta ya zuba mata harshensa cikin yana sarrafa harshenta har tsayuwa tasoma neman gagararsu dan duk jikinsu rawa yake zubewa sukayi akan gado "baby idan kika bada mugudumuwar tayewa zukatanmu abinda suke muradi komai zai iya faruwa .....

wani irin sakonni na musamman yake aika mata , masu wuyar misaltuwa, ta yadda take jin duk duniya idan ba M. A bazata iya rayuwa da kowa wani d'a namiji ba, yaron ya lakanci sirrin sarrafa mace takowani bangare , duk inda ya kai hannunsa ajikinta sai taji wani irin zirrrrrr gashin jikinta su mike komai ya nemi tsaya mata, kmr yadda take jinta a yanzu ajikinsa..
a d'akinta ma kusan raba dare sukayi yana murzata da romancing din jikinta kafin daga baya ya baro d'akin yana layi tmkr wani mashayi gbdy yanayin idanunsa sun sauya haka ya wuce ya koma bangarensa ya zube kan kujera..

****
muwaddat ta matsawa ummi akan tafiyarta Wanda Sam auwal bai sani ba dan tun dayaji ummi tayi shiru ya d'auka ta bar zance ne, gbdy M. A ya kasa boye abinda ke cikin ransa ,ya matsa muwaddah sosai gaban kowa mata
yake nuna tsananin sonta ,
Wannan dalilin yasa Ummi ta soma shirye shiryen
tafiyar muwaddat gurin iyayenta ta k'arasa hututa acan ,domin har takira ta sheidamusu...

still free page

domin bukatar karanta labarin muwaddat zaki biya 300 naira ta wannan account din 2175076611 zenith bank aishat abdullahi, idan kin biya zaki turawa wannan number 08032384602 domin tabbatarwa ,idan kuma katin mtn ,ko Etisalat ko glo zaki turo ,zaki tura ta wannan number 08059623096

Mmn sudais ce
2/4/20, 8:39 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~
AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

warning!!!

don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

page 12

.....washegari da ummi zata tafi hospital tace" muwaddah ta shirya suje ta duba lafiyarta ,duk wani abinda ya kamata ummi tayi mata tayi ,inda ta gano muwaddah bata d'auke da cutar komai ajikinta, illa malaria wanda mostly daman ita ke haddasawa mutun ciwon kai mai tsananin, allurai tayi mata har guda uku da magunguna, da kyar muwaddah ta sha tana zuba shagwa'ba ,byn ta sha maganin ta samu guri ta kwana akan gadon dake ajiye a office din ummi...

sai gurin azahar suka koma gida ,muwaddah nata jiran ummi tayi mata zance tafiyarta ilori aranar dan ita har tagama shirinta tun daren jiya, amma taji ummi ta share da zance, sai ma gayyatar M. A asibintinta data ji tana yi ,"bunayya ina son gobe idan Allah ya kaimu ka shirya ka fara zuwa asibiti domin taimakamin da wasu abubuwa kafin lokacin komawarka yayi.

tsadadden murmushin nan nasa yayi mai tafiyar da ruhi saboda dimples dinsa dake lotsawa a duk sanda yayi, hakan ke sake fito da ainihin kyawun halittar da Allah yayi masa ,ahankali ya motsa la'b'bansa tamkar mai koyan mgn yace "kai ummi yaushe zan kama zuwa wani asibiti , ai wannan asibintin naki sai ke, ni aikina ya wuce zuwa wannan asibintin naki ,ko kin manta

abinda na karanta ne ummi ?
"idan kin manta ummi bari na tuna miki d'anki muhammed auwal ishaq orthopedic sugyren ya karanta a kasar london tsadadd'en
course din nan wanda samun likitoci irinmu ke da wuya a wannan lokacin ,ni yanzu idan ba gani nayi fuskar mutun tayi damage ba,jikin mutun yayi dagadaga ba , ko bangaren macen da brest dinta ya zama tsuma , ni kuma nayi k'ok'arin naga na maida shi na yarinya kmr muwaddah da saurarans u, bazan tsaya wani 'bata lokacina akan wasu abubuwa ba, miwaddah najin haka taja tsaki aikinka kenan duk maganarka bata wuce nono tayi mgnr a kasan ranta tana kawar da idanunta daga garesa..

Ummi tace "Allah ya shiryeka bunayya, ban da abunka ai zaka iya zuwa, baza'a rasa wanda zaka taimakawa ba, tunda kullun da irin matsalolin da muke fuskanta asibiti.

"a'a ummi bafa zani wani asibinti domin yin allura da k'arin ruwa ko cs da dai abubuwa makamantansu ba, amman idan kun samu abinda ya danganci aikina kuna iya kirana....

ummi ta ba'ta fuskar tace "wannan girman kan naka da son girma nan ke had'ani da kai wallahi, bansan inda ka samo irin wannan halin ba , mahaifinka sam babu ruwansa , "haba ummi ki dai sake magana karki ce baki san inda na samu halaiyeta ba, ai ni komai nawa na abi ne babu wani banbaci atsakaninmu sai abinda baza'a rasa ba,kuma ina alfahari da hkn ya k'arasa maganar yana murmushi tare da kallon inda muwaddah ke zaune, wacce ko kallon inda yake bata yi ba..
haka suka yita hirarsu ta tsakanin uwa da d'a, yayinda muwaddah
tayi shiru tana saurarans u, dataji hirar ta isheta ta mike ta koma d'aki,
bayan tafiyarta ummi ta sake fuskantarsa sosai da zancen ,da kayar dai ta samu ta shawo kansa ya amince zashi a gobe..

washegari wuraren shabiyu saura ummi ta kira layinsa saboda taji shi shiru har lokacin bashi da ala'mun zuwa ,lokacin da kiranta yashigo wayarsa yana makale da muwaddat a d'akinta yana rud'ata da salon wasaninsa masu tsayawa arai da wuyar mantawa , mikewa zaune yayi daita ajikinsa ya zaunar daita akan cinyarsa ,tayi yunkurin tashi Amman ya rike hannuta gam cikin nashi yana murzawa ahankali ahankali, sannan ya lalu'bo wayar acikin aljihun wandosa yana dubawa, kafin daga bisani ya d'auka muryarsa a kasalance yace "ummi .....
"Wai bazaka zo bane bunayya?
" zanzo mana ummi "

ummi tace "to ai naga har to 12 yanzu banganka ba "karki damu ummi nah gani nan zuwa yanzu just give me some minit "to shikenan d'an albarka ina nan ina expecting din zuwanka,ya katse kiran ya kwanta flat akan katifar tare da fixgo muwaddah samansa ,sai gata ta haye ruwan cikin suna fuskantar juna ya had'e fuskarsu yana busa mata numfashinsa mai gauraye da hucin sha'awarta kana yace " muje ki rakani asibitin gurin ummi, ta girgiza masa kai ala'mun bazata ba.

"ba zaki ba?
tace "ka tafi dan Allah ina son na huta ,hannuwansa duka yasa ya kamo fuskarta ya d'aura lip's dinsa akan nata yana yana yawo dashi kafin daga baya yasoma k'ok'arin tsotsa lis'p dinta ,tayi saurin kawar da fuskarta gefe tana fidda numfashi sama sama tare da cewa"i don't like it bunayya, banason abinda kake min, abubuwan da kake min kwanakin nan sun fara damuna plz control your self.. ..
tana gama fad'ar haka ta kai hannuta kirjinsa tana k'ok'arin mikewa tsaye,bai mata komai ba har tagama mikewa ta tsaya tare da jiya masa baya shi kuma ya tashi da kyar yana gyara zaman rigarsa ya fice daga d'akin.

Tana ganin fitarsa ta sanyawa kofar d'akinta key ta koma tayi kwananciyarta tana fidda numfashi sama sama dan ita kad'ai tasan yadda take ji ajikinta a duk sanda suka kasance tare .

 ahankali M.A yake direving yana tunanin muwaddah, har ya k'araso tangamemen asibintin ummi wanda ya amsa sunansa saboda tsaruwar da yayi, amman still tunanin muwaddah yaki barin cikin kwal'kwaluwarsa, yarasa wani irin zazzafan kauna take mata ?
Ya rasa me yasa yake sonta irin hk da har yake jin idan ya rasa arayuwarsa zai iya mutuwa ?

M. I profetional hospital shine sunan hospital din ummi , kai tsaye gurin da'aka tanada domin ajiye motar M. D ya nufa yayi parking din motarsa a daidai lokacin da wasu daliban likitoci suka fito harabar asibinti sanye da fararen kaya , "basma Kalli motar can inji cewar kausar tana matsa yatsun hannun da karfi , basma a d'an kid'eme ta tsurawa tsaleliyar farar motar mai bakin glass idanun tana kallo har lokacin da M. A ya fito daga cikin motar sanye da farin riga da wando jeans baki ,sai bakin glass dake manne da idanunsa kallo daya yayi musu ya d'auke kansa akansu ya soma neman layin ummi kira daya ta d'auka "ya'akayi bunayya ka k'araso ne?
"eh ummi "okay ka bani minti biyu zansa a taho da kai, "haba ummi duk matsayina ,maimakon kizo da kanki shine zaki turo wasu , ni dai dan Allah kizo da kanki kinji ummi nah"to shikenan gani nan, ya katse kiran tare da maida wayar cikin aljihunsa ya rungume duka hannuwansa akirji yana jiran fitowar ummi ,yayinda har lokacin basma da kausar idanunsa ke kansa suna santin irin kyawun dayake dashi..

"ummi ta fito da kanta tarban tilon shagwa'ba'bben d'anta , hakan kuwa yayi masa dadi sosai ya sakar mata murmushi ya riko hannunta"ummina ina sonki dayawa ...
 "Nima haka yarona ina sonka fiyye da yadda kake sona , tare suka jera zuwa cikin asibinti suna mgn kasa kasa , duk inda suka gilma sai an gaishe da ummi cike da girmamawa ,ita kuma sai nunawa mutane M. A take , ga yaronta dake karatu a London, haka mutane sukayita gaishe shi yana amsa musu a dake cike da miskilanci, har suka k'arasa office din da'aka tanada dominsa .

ummi tana murmushi tace "bunayya ga office dinka dake, zaman jiranka ..

ahankali ya saki murmushi yana karewa office din kallon ,komai yayi babu abinda babu ,hadadd'en office ne wanda ke d'auke da makeken table zagaye da mazaunin likita, sai kujera guda biyu dake fuskanta ta likita Wanda idan akayi baki zasu zauna akai , daga can gefen kuma gadon duba marasa lafiya ne zagaye da farin labule ,da extra room, sai bayi da tangameman hotonsa wanda yayi a gurin graduation dinsa a London,daga bangaren gabas kuma daddumar sallah ne,sai karamin frame din hoton abi da ummi shi kuma yana tsakiyarsu a gefen calander, sai kamshi office din yake yi tamkar daman akwai Wanda ke aiki acikinsa , naunayen ajiyar zuciya ya sauke had'e da lumshe idanunsa ya juyo ya kalli ummi byn ya karewa office din kallo "ummi nah na gani na gode kuma na yaba sosai komai yayi kmr yadda nake bukata ,Amman nifa ba aiki zanyi ahalin yanzu ba.

"nasani bunayya,nasan ba aiki zakayi ba amman ina son kasan da zamansa, saboda ina son anan zakayi aikinka tare dani idan ka had'a master's dinka, ya zagayo bayanta ya d'aura habarsa a kan kafad'arta yace "shikenan ummi nah tunda hk kike so bani da yadda zanyi ...ummi tayi murmushi ta shafo fuskarsa tace "haka nake son ji ,Allah yayi maka albarka "ameen umminah,suka fito tare daga cikin office din ummi ta rufe ,ahankali suke takawa ummi na zagayawa dashi cikin asibintin har kusan la'asar sannan ya fito da zumar komawa gida anan ya sake cin karo da basma da kausar ya kallesu ,suma kallonsa suke ,ya kawar da fuskarsa yashiga motarsa ya figa aguje ya nufi bakin get.

basma ta juyo ta kalli kausar "gsky mai motar nan ya had'u dayawa haka ma motarsa ya hud'u "wallahi kamar kinsa abinda nake son fad'a kenan koda yake kyawunsa bana banza bane mahaifiyarsa akwai tsabar kyau ,kausar tayi shiru saboda kyawunsa da had'uwarsa yafi karfin tunaninta ,ina ma ta samu irinsa , saboda irin mijin datake muradin samu kennan arayuwata, sai dai sama tayiwa yaro nisa sai dai ya d'aga kai sama yayi kallo,ina ita ina auren d'an M. D, mukarama, tun tana sauraron surutun basma har tazo bata fahimtar komai ..

****

Sai daya jera kwana biyu yana zariyar zuwa hospital din ummi bisa tursasawarta ,sai dai babu abinda yake sai zaman office dinta da latse latsen waya ,kwana na uku yace bai zuwa gidansu nabeel zashi , duk yadda ummi tayi dashi yace bai zuwa haka ta hakura ta barshi .
cikin kwana na biyar ummi ta kirasa cikin tashin hankali muryarta kmr zatayi kuka byn ya d'auka tace "bunayya kana ina kazo hospital yanxu Yanzu dan Allah?
Shima cikin matsanancin tashin hankali yace "lafiya ummi ,me ya faru ?

"kai dai kazo yanxu ta katse kira, batare da 'bata lokaci ba ,ya fito cikin Sauri rigarsa a hannu yana k'ak'orin sakawa, a daidai bakin motarsa ya k'arasa saka rigar ya bud'e motar yashiga ya zauna yana kunna motar hade da danna hon da karfin gaske .

Yana isa a harabar asibinti yayi parking yana k'ok'arin fitowa daga cikin tsaleliyar motarsa sukayi kicibis da kausar sanye cikin uniform ,ahankali ya fito daga cikin motar yasoma tafiya cikin takunsa na d'aukar hankali, ta tsura bayansa ido tana kallonsa tana jin ina ma yazamo

mallakinta ,jikinsa ne yabashi kallonsa take dan haka ya waiwayo shima yana dubanta sai dai nashi kallon da gani na tsantsar tsana ne tattare da takaicin kallon datake masa ,yaja tsaki ya girgiza kai kawai ya wuce saboda arayuwarsa ya tsani irin wannan kallon da mata ke masa ,kusan minti goma tayi a dan kare agurin tana kallon bayansa ...
Tun daya shiga emergency hankalinsa ya tashi matuka sakamakon kukan da tarar da wasu matune nayi , Allah Allah yake ya isa office din ummi yaga halin datake ciki a daidai bakin kofar shiga office dinta suka had'u ta riko hannunta cikin azama ta nufi d'akin tiyata dashi bai ce komai illa binta dayake ahankali har suka shigo d'akin dake cike da manyan likitoci ..
Suna ganinsu suka ja baya suna duban yaron da ake tunanin shi zai duba mara lafiya .

abinda ya gigita ummi har yasa ta kirasa cikin tashin hankali ,shi sam bai d'aga masa hankali ba, saboda inda sabo ya rigada ya saba ganin irin irinsu agurin practical ,wata k'aramar yarinya ce kwance akan gadon marasa lafiya a d'akin tiyata wacce shekarun haihuwanta bazasu wuce shahud'u ba a duniya , tana fidda numfashi sama sama ranta hannun Allah, sai dai gabad'aya fuskarta tayi damage,sakamakon 'yan ta'ada da suka kawowa mahaifinta ta hanyar kawo masa hari ,saboda ba'ason ya zarce kujerarsa ta d'an majalisar jahar dayake kai , sukayi rashin sa'a basu samesa a gidan ba ,wannan bakincikin yasa sukayi tillon diyarsa fad'e sannan suka watsa mata acid a fuska .

ahankali M. A yake kallon yarinyar yana girigiza kai , yana sake mamakin wannan tashin hankali da maseefar son siyasa irin ta mutanen nigeria,akan siyasa babu abinda bazasu iya yi ba, ya tausayawa yarinyar sosai ,batare da bata lokaci ba ya bukaci kayan aiki yana cigaba da dubanta tare da tunani ta inda zai fara ,cikin rawar jiki ummi take bada sauran likitocin umarni ,cikin kankanin lokaci M.A yashiga taimakawa yarinya cikin gaugawa, yayinda manya likutocin dake aiki a asibintin suka zagayeshi suna taimaka masa , ban da ummi wacce tuni ta fice daga d'akin din dan ta kasa tsayuwa saboda yadda fuskar yarinya yayi dan nama fuskarta har yasoma zagwanye.. ..

sosai M. A yashiga k'ok'ari akan yarinyar, domin taimakawa rayuwarta, sai dai duk wannan aikin da yake zuciyarsa na bugawa saboda wannan shine karo na farko da zai yi aikin daya danganci haka.
bashi ya fito daga d'akin tiyata ba sai gurin shida na yammacin rana, inda har lokacin iyayen yarinya sun kasa tsaye sun kasa zaune sai zariya suke suna rusa kuka,ta gabansu yazo ya wuce, kai tsaye gida ya wuce saboda ya gaji dayawa,yana zuwa gida bathroom yashiga ya sakarwa kansa shower ya gama ya d'auro alwala ya fito ya tada sallah ,byn yayi sallah yaso ya kwanta saboda wani irin bacci yake ji amman sanin da yayi bacci a daidai wannan lokacin bashi da kyau ,yasa ya koma parlour'nsa ya kwanta flat akan kujerar kushin me zaman mutun uku ya d'auki remut ya kunna TV ya janyo wayarsa ya kira cikin gida a kawo masa coffee ..

****

ranar bacci M. A yayi sosai can gurin asuba wayarsa ce ta tashesa daga bacci kiran gaugauwa daga asibintin ummi yana d'auka "yace muhsin ya'akayi? Muhsin daya daga cikin likitocin dake

aiki ne asibitin, yace
"daman yarinyar da akayi wa sugyren din ce fa har yanxu bata motsa ba, M.A yasa hannu ya d'auki agogonsa yana duba lokaci ,yace" okay nan da awa daya idan bata motsa ba ka bari nasani "okay...

Muhsin bai kira ba sai byn awa ya sake tabbatar masa fa yarinyar har lokacin bata farka ba ,bashiri ya mike ya shirya ya bar gidan xuwa asibiti ,akan hanyarsa ta zuwa asibiti ya kira ummi yake fad'a abinda ya faru tace"nima yanzu nake shirin kiranka sai gashi ka kira Allah dai ya bada sa'a yasa ayi nasara aiki "ameen ummi ..

 .....muwaddah kuwa tunda taji wayarsa da ummi hankalinta yayi matukar tashe saboda ummi ta bata labarin abinda ya faru jiya ,jikinta yayi mugu mugun sanyi dan batason ya samu matsala da aikinsa, gabad'aya a sanyaye ta dinga abubuwanta, ganin haka yasa ummi tashiga rarrashinta tana bata baki akan tayi hakuri" cikin kwanakin nan zata shirya mata tafiyarta zuwa ilori , dan a tunaninta kodan saboda haka ne yasa tayi sanyi taki sakin jikinta .

shi kuwa auwal tunda ya isa asibitin bai samu zama ba,sai kai kawo yake ,har sai da yarinya ta farfad'o tukunan hankalinsa ya kwanta ,batare da 'bata lokaci ba ya kira ummi a waya ya sanar mata, murna tayi sosai had'e da jiro masa addua , tun safe hankalinta bai kwanta ba sai yanzu daya kirata .
byn sun gama waya ta dubi muwaddat dake zaune tana kallon zeeyword.
 " muwaddat ta kira sunanta cikin farinciki" "na'am ummi ta amsa tana dubanta "kinji bunayya ya samu nasara akan aikin nan "

murmushi tayi cikin sakin fuska saboda har ga Allah taji dadi sosai ,ahankali ta motsa labbanta tace"Allah yasa yafi haka "amen inji cewar ummi muwaddat tacigaba "ai jikina ya bani tabbas zai yi nasara saboda bunayya nada matukar kwazo .
"Haka ne Amman da fari naji tsoro sosai saboda karonsa na farko kenan "haka ne Allah dai ya taimaka.
  Ummi tace "ameen tare da cewa yauwa bari na aikeki gidan alhj nuhu ki kaiwa hjy kubura wad'an nan atamfofin da kamfala,ai duk kalolin da kika d'auka sun miki ko?

"sun yi min ummi, sai dai ni kamfalar nafi so wallahi, ina jin kmr na had'esu duka na dinka dogayen riguna dasu, dan babu wace kalarta batayi min kyau ba "
"Allah shalelen umminta da abi ..?
Muwaddat tayi murmushin tace "da gaske nake "to ai shikenan bari abarsu kawai ki sha kwaliyarki dan nafi son kullun nayita ganin ki tsaf tsaf ,sai ki maida mata da atamfofin .
muwaddat ta mike ta amshi farar ledar dake rike a hannun ummi "tana lekawa ,"ummi naga ke baki d'auki kamfalar ba?
ummi tace nifa bawani damuna tayi ba, nafi ga atamfar dai.
muwaddat ta cire kamfalolin ta ajiye akan kujera, ta kama hanyar fita "karki dade kije yanzu ki dawo kafin abi ya dawo, kai kawai ta daga mata ta k'arasa ficewa.

kai tsaye inda ummi ta aike ta nufa,tana shiga gidan, da mijin hjy kubura tasoma cin karo a harabar gidan yana zaune rike da jarida daily trust, gabansa k'aramin tebur ne mai d'auke da tattaciyar ruwan inibi da ruwa ,sai ritsetsen tubinsa mai kama dana yan giya.
sallamarta yasa ya bar abinda yake ya d'ago ahankali yana kallota ,har ta iso daf dashi bai d'auke idanunshi daga gareta ba, ta bude baki da kyar ta gaishe shi "ina yini ?

da sauri yace lafiya lau muwaddat yammata ya gida da hutun makarata ?
"lafiya lau ta bashi amsa atakaice tana tafiya batare da ta sake kallon inda yake ba. shi kuma yabi bayanta da kallo cikin rausayar da kai, shi dai muwaddat tana matukar burgeshi duk sanda ya ganta sai yaji wani abu ya tsarga masa ,yana son tukararta amman babu fuskar da zai bayyana mata abinda ke cikin ransa, ahankali ta k'arasa cikin gidan inda ta iske hjy kubura zaune tana kallon tashar arewa 24 ta gaisheta tare da mikawa mata afamfofi tace "gashi inji ummi tace na kawo , hjy kubura ta amsa tana murmushin jin dadi ganin duk an kwashe rabin kayan ,muwaddat ta juya abunta tasoma kokarin barin parlour'n ,hjy kubura ta ajiye laidar a gefe tace "ki gayawa ummintaki zuwa anjima idan na natsa zan kirata..muwaddat tace
"to ,tacigaba da tafiyarta.

inda tabar alhj nuhu zaune a nan ta dawo ta iske shi yana kallon kofar shiga cikin gidan ,bata ko kalli inda yake ba saboda tsarguwa datayi dashi, dan sam batason yawon kallo arayuwarta koda ta juya baya tana takawa ahankali jikinta na bata idanunsa akanta suke,shi kuwa ahji nuhu ido ya tsurawa bayanta tare da sauke ajiyar zuciya yana lasar lips dinsa da tuni suka fara bushewa ,da sauri ya mike daga zaune dayake ya biyota, wanda lokacin tuni har muwaddat ta kai kofar get din gidansu , ya tsaida ita cikin tsarkewar muryar yana kiran sunanta "muwaddat muwaddat!! ....

taja ta tsaya tana juyowa ahankali tare da tsare gira da had'e fuska sosai "tace menene?
sai da gaban alhaji nuhu ya buga saboda firgicin daya ziyarcesa ,duk da yadda zuciyarsa ke bugawa hkn bai hanashi k'arasowa inda take tsaye ba, ya d'an lumshe idanunsa yana fad'ad'a fuskarsa "uhm ammm muwaddat daman ina son na d'an miki wani bayani ne gsky akan wani lamari mai girma dake zuciyata , wato muwaddat na dan jima ina son bayyana miki sirrin dake raina akanki "
tayi shiru tana sauraronsa har sanda ya numfasa sannan yacigaba "muwaddat azahirin gsky idan kin kalli cikin kwayar idanuna zaki iya fahimtar inda zancena ya dosa tayi saurin katsesa " ni ban fahimci komai akan zancenka ba "ya gyara tsayuwa yana rungume hannuwansa akirji ga kuma ritsetsen cikinsa "eh to daman dai na dad'e ina sonki kuma aurenki nake son yi idan kin amince"

idanunta ta rausaya cikin nasa dariya na neman kufce mata a yadda take kallonsa da ritsetsen tunbinsa, da jajayen kwalala idanuwansa kmr na agolan nafawa, hancinsa a zube kmr faranti yasa dryar ta k'arasa kwacewa dry tana rufe bakin da hannuwanta .

take alhji nuhu yashiga kallon jikinsa yana dubanta, gabadaya ya rasa driyar me take masa

,ita kuwa sai dariya take gabadaya bata ta'ba ganin abinda ya sata dariya ba irin maganar alhj nuhu ,ta kalli wannan ritsetsen cikin nasa tana sake kwashewa da dariya gabad'aya mutun babu fasali Amman yace wai ita yake so..
alhji nuhu na dubanta yace "nasan kina dariya ne saboda kina ganin kmr nayi miki tsufa ko ? Ya fadi hk saboda shi in da tuninasa yaje kenan , ya numfasa kana yacigaba da mgn "ita soyayya da kike ganinta muwaddat babu ruwanta da wannan, ni dai ina sonki tsakani ga Allah idan har kin yarda kin amince zan gabatar da kai....
A matukar tsawace tace "dakata dan Allah baba zance komai me ni ban ma San abinda zan kiraka dashi ba ?

"duk wanda kika fad'a bazai dameni ba matukar zaki soni ki aureni .
ta sake kwashewa da wata dry adaidai wannan lokacin motar M.A ta karyo kwanar unguwar , ahankali yake driving ciki hadaddiyar motarsa baka wuluk kirar tucsion 4wd, tunda ya karyo idanunsa ya sauka akansu tana dry shima alhj nuhu na murmusawa , annurin fuskarsa ta d'auke, zuciyarsa tashiga dokawa, muwaddah ta kasa tsaida dryar har zuwa sanda M.A ya k'araso kofar gidan wanda zuciyarsa bata daina bugawa ba ,ita kuma ganinsa bai sa ta daina driyar da take ba .

parking yayi ya fito batare daya tsaya rufe motar ba ya zuba duka hannuwansa acikin aljihun wandonsa yasoma takowa ahankali zuwa inda suke, sai lokacin gabanta yashiga dukan uku uku saboda irin kallon kaskancin daya aiko musu dashi dip dariya dake bayyane akan fuskarta ta 'bace ,yana gama k'arasowa alhj nuhu ya juya da niyyar barin gurin tunda yana da labarin yadda M.A yake korar mata samari, har yayi taku biyu M.A yace "no baba ka dawo muyi magana ta kunne da kunne da kai alhji nuhu ya d'an dawo ya tsaya yaji me zaice .
M.A ya dubesa a wulakance yace "wannan shine karo na farko dana ganka tsaye da wannan ? "me kawoka gurinta?
muwaddat tayi saurin dubansa "itace ma wanna kmr wanda bai san sunanta ba..
shi kuwa alhji nuhu tsuru yayi da ido yana kallon kwayar idanu M.A dake cike da tsantsar kishi kafin daga bisani yace "wai da sonta nake amman dai karka damu zan yiwa shi mahaifin naku magana "you are very stupid kai da mganar da zaka yi masa "ni kace wa stupid?
"ance maka stupid more than donkeys, banda buduwar zuciya irin taka shekararka nawa shekararta nawa a duniya da zakace kana sonta kuma har da aure?

" to wannan yazama karo na farko da karshe da zan sake ganin kafarka a kofar gidan nan da sunan kazo zan.. "bunayya ..... muwaddat ta kira sunansa cikin rawar murya ya kake k'ok'arin yin abinda bai dace ba nifa ba son nake ba "shiiiiiii bana son jin komai ya katseta "ina sane sarai ba sai kin fad'a min ba kya son wannan mutumin mai tubi kmr tulun giyya ba.....

alhj nuhu ya fusata sosai cike da kunfar baki yace "kai a she baka da kunya, ina ganinka kmr yaro kirki a she d'an iska ne ban sani ba?
"kwarai kuwa na wuce haka akan wannan ya nuna masa inda muwaddat take tsaye da yatsan hannusa "ai kuwa zaka gane baka da wayo ,ba dai ni kayiwa wannan iskanci ba ?

"Ai sanin babu abinda zaka yi yasa nayi maka , abinda nake so da kai ,ka rike girmanka ka daina d'aura idanunka akan abinda bazaka iya dashi ba, koda kuwa ya zama mallakinka ...

fuuuuu alhj nuhu ya juya ya nufi cikin gidansa yana suritai "aikin banza kawai kananan yara daku sai iskancin banza da wofi ko an ce maka tashen balaga hauka ne, idan kaima sonta kake ai sai ka fito a gabza da kai , ba ka tsaya rainawa mutane wayo ba ,yana mgn yana k'ara sauri dan kar M.A ya jiyosa ya tara musa jama'a a da ya lura yaron bashi da kunya"

M.A ya kalli muwaddat yace " ke kuma ya nuna ta da yatsansa "sai wani bud'e masa baki kiyi kina washe masa hakora "a'a to makeke son nayi ni wallahi dariya yabani "babu wani idan kina sonshi ne tun wuri ki cire hkn aranki ,dan ki sani an haifeki ne saboda ni, nima kuma haka, dan haka wallahi zamuyi mugun samun matsala dake idan kina tsayuwa da irin wannan tsofofin da duk basir yagama rakikesu, babu fa abinda zakiji airinsu alhj nuhu da alhj jibirl ,ki tsaya irinmu mune zamu baki abinda zai sa kiji kwanciyar hankali, amman idan kinji kina son shi shikenan tunbisa ma kawai ya isheki juyawa tayi a matukar fusace tashiga gida tana jan tsaki .

Zaune ta iske ummi da binta mai aiki a palour cikin hiran jin dad'i
da nishad'i ta zauna tana huci "ummi tace lafiya ke kuma kika shigo kina nimfarfashi?
kasa magana tayi, binta data ga hk tayi murmushi "yar gidan umminta wa ta'bo mana ke?
Ko rufe baki batayi ba M.A ya shigo cikin miskilanci yace "ni ne kuma nasan babu abinda za'a iya min ya k'arasa mgnr tare da zama gefen
ummin yana
tab'e fuska yana ta huci.

binta ta kwashe da dry "lallai kam babu abinda za'a yi, domin kuwa babu mai shiga tsakaninku, Allah dai ya huci zuciyoyinku.. M.A
ya kalli muwaddat dake gefe ummi rik'e da kuncinta tana dubansa daga kallon datake masa ya fahimci yadda ranta ya 'baci ,shima tsumammun idanunsa ya tsura mata cikin had'e fuska yace, ummi
"Wlh ni baby kunya take bani ,da irin mutanen da suke zuwa gurinta da sunan so ummi tayi murmushi me kuma ya faruwa su wad'ane mutane zaka fara ko?

"babu wani zan fara ummi wai yanzu ina dawowa na ganta tsaye da wancan shashan tsohon yana tsarata abun gwanar kunya ita kuma sai washe masa baki take ..
Ya maida idanunsa akanta yace " yanzu dan Allah bby kirarsa bata razanaki ba "wallahi ni da mace nake irin su alhj nuhu, alhji jibirl basu taba samu kofar da zan tsaya dasu ba.. ummi tayi dry "kai dai babu ruwanka da samarinta..
Ita kuwa muwaddat harara ta watsa masa cikin 'bacin tace "ina ruwanka to?
" ai gara auren irinsu da auren yara kanana ....."wallahi karya ne bama zaa taba hadawa ba ki dai canza tunani wallahi wadan tsafafin babu abinda zasu miki ..
ta juya ta kalli ummi..

" ummi kiyiwa yaron nan magana ya fita daga harakata da lamarin gabadaya, nifa shiyasa wani lokacin har banason ya dawo kasar nan, gara muyita gaisa a waya dashi .

"karya ne yarinya..wannan mgnrki karya ce wallahi ,ni nasan kusan kin fi kowa jin dadi dawowata ,saboda abinda ido da ido zai gane bazai kai kunne da kunne ba ko ba hka ?

Muwaddat tace "ba'asani ba ,ni dai ka daina shiga rayuwata da samarina ta k'arasa mgnr cikin tsigar wasa, duk Wanda yazo gurina sai ka korensa ko ni Sa'ar wasanka ce"?

bata kai ga rufe baki ya taso cikin fushi ya tsaya gabanta yana nunata jikinsa har rawa yake yace "an koresu din sai kiyi abinda zakiyi ,wallahi sau d'ari zan ganki da irinsu alhj nuhu sai na koresu yana gama fad'ar hk ya juya fuuuuuuu ya bar parlour'n..

ummi tabi bayansa da kallo tare da cewa "binta taya ganin karfin hali ,Anya kuwa bunayya na cin hankalinsa?
" ji yadda yake wani hakikancewa kmr wani ubanta ko mijinta .?
ummin na gama fad'ar hk ta mike zata bi bayansa muwaddat tayi saurin riko hannuta "haba ummi wasani fa, nifa da wasa nakeyi wallahi har ga Allah banji haushinsa ba....

ajiyar zuciya ummi ta sauke sannan ta koma zauninta tace "duk da hk dai rainin hankalinsa na neman wuce iyaka "hakuri zakiyi hjy tunda ita muwaddat din tace wasa ne, kin kuma san da wannan yar tsamar atsakaninsu daka ce ma shine yayanta da auren zumunci za'a yi inji cewar binta tana murmushin.
ummi tayi sauri "tace a'a ban ciki da wani auren zumunci yaje can ya nemo Matarsa itama haka, ina dalili, daga yanxu kar ki sake yarda ya dinga kore miki samari...

suna cikin magana abi ya daga labule yashigo da sallama, muwaddat ta mike ta amshi jakar hannunsa da ledar hannunsa, ta mikawa binta dake tsaye ledar tayi masa sannu da zuwa ta nufi d'akinsa itama binta tayi masa sannu da zuwa tayi ta kama gabanta..

Abi ya k'araso ya zauna kusa da ummi "hubbey fad'an me naji kina yi haka kuma ke dawa?
"sannu da zuwa, ni da wa inda ba da wannan d'an naka ba?
abi yayi murmushin me kuma auwaluluna yayi?
nan tashiga zayyano masa abinda yayi ...
"to ayi masa afuwa a yafe masa shima watakila yana da dalilinsa na yin hakan, yanxu dai ina bukatar ki saki fuskarki domin itace karfin gwiwata ummi tayi murmushi "kai ko, duk lokacin da ake serious issue sai kasan yadda ka shashantar dashi..
muwaddat ta dawo parlour'n rike da tire mai d'auke da ruwa da lemu mai sanyi ta tsiya acikin glass cup ta mikawa abi "yauwa muwaddat sannu da kokari ya gida?
"lafiya lau abi ya aiki ?

"alhamdullahi ta juya ta nufi kitchen.. ya d'an kurbi ruwan lemu yana duban ummi "har yanxu banga fuskarki ta dawo min tmkr yadda nake so ba ,idan tacigaba da zama haka zanje na tsilla wankana na tafi zance .

"daman yau nayi babban kamu har cikin ma'aikata ,yar yariya fara sol dagowa wacce zata gyara min tsufana "suka sa dariya atare ummi tace "ya rabbi..ni dai tashi muje daga ciki.. ta mike tayi hanyar d'akinsa ya biyo bayanta muje din tare da cewa "kinsa surajo mai aiki a kafanina .. ?
"wani surajo vice chiaman na kamfaninka?
"shi kuwa da sauri tace "me yayi Allah dai yasa ba sallamarsa zakayi ba?

"ina ai surajo yafi karfin da kamfani zata koresa saboda himma da hazakarsa tare da rikon amanarsa, bari dai nayi wanka na fito, "okay tashiga taimaka masa ya cire kayansa yashiga bayi ta rufo masa kofar ,ta karasa gaban wordrobe dinsa ta bud'e ta fito masa da jallabiya black colour...

Free page

Domin bukatar karanta labarin muwaddat zaki biya 300 naira ta wannan account number din 2175076611 zenith bank Aisht Abdullahi,idan kinbiya zaki turawa wannan number 08032384602 domin tabbatarwa ,idan kuma katin mtn ne ta wannan number zaki tura 08059623096

Mmn sudais ce
2/4/20, 8:39 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

warning!!!

don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

page 20

....Tun bayan fitar bunayya daga d'akin abi,abi ya kasa samun natsuwar zuciya a game da al'amarin tillon d'ansa,
" a zahirin gaskiya yana jin tamkar ya biye masa ne, yayi masa abinda ya bukata, amman lokacin daya tuna shekarunsa a duniya a halin yanzu sai yaga gabadaya lamarinsa na tattare da kuruciya da sharrin soyayyar farko ne , Wanda mafi akasari akan samun haka acikin wannan duniya .

soyayyar kuruciya mafi yawa matasa na tsintar kansu ciki wannan shaukin mai wuyar misaltuwa Wanda da wuya akai ga cimma burinta,
Dan haka ya ajiye maganarsa amatsayin yarinta da kuruciya ne kawai ke dawainiyya da d'an nasa ,bancin hk ta yaya kamar bunayya zai ce ayi masa aure a wannan lokacin
"auren ma da wace ta girmesa?
tattara zance yayi ya ajiyesa amazaunin wasan yara da kuruciya , ya cigaba da abinda ke gabansa .

Shi kuwa bunayya Ko daya dawo d'akinsa ya kasa samun sukuni, gabad'aya ya rasa abinda ke damunsa, zuciyarsa banda tafarfasa babu abinda take, ya kasa zaune, ya kasa tsaye, sai zariya yake acikin d'akin rike da kugunsa yayinda hannusa daya ke dafe da goshinsa ,gabad'aya hankalinsa baya gangar jikinsa, 'kwa'kwaluwarsa ke hasko masa wai ga muwaddat dinsa can tare da ala'meen tana masa murmushin nan nata da yafi so da kauna akan komai acikin duniyar nan ,take wani zazzafan kishi ya turnuke zuciyarsa dama gangar jikinsa, ahankali ya runtse idanunsa yana girgiza kai, kirjinsa na wani irin dokawa da sauri " Impossible ya furta a bayyane had'e da bud'e idanunsa ya cigaba da zagaye d'akin ..

"Anya kuwa zan iya d'aukar lokaci batare da na kai kaina gareta ba ?
Anya ba wani abu al'amen yake nufi dashi ba ?
"to wai ma me taje yi d'akinsa a daidai wannan lokacin?

"Ko ba'a gaya masa ba yasan ala'meen son muwaddat dinsa yake, tun da shi ba makaho bane ,dan idanuwansa sun fara hango masa mugun nufinsa akanta ..
Abinda yakamata kawai kaje ka d'aukota ka dawo daita gida shine kawai besty solution da kwanciyar hankalinka gareka ,zuciyarsa ta umarcesa da fad'ar Hakan ,take kuwa ya amince da shawarar zuciyarsa ,ya kudirci aniyar ko bai je gobe ba kamar yadda ya furta mata ba, to kuwa cikin satin sai ya dangana da ilori ,duk ma abinda zai faru sai dai ya faru amman sai ya d'auko abarsa kafarta kafarsa ya k'arasa maganar yana
fad'awa Kan makeken gadonsa da karfi ya kwanta ruf da ciki , yana furzar da iska mai zafi had'e da shafa sumar kansa ,sannan ya kai hannunsa ya janyo wayarsa shiru yayi sakamakon ganin har lokacin wayar tana kan layi ba'a tsinketa ba.

ya sauke naunayen ajiyar zuciya yana duban screen din wayar sannan ya kai wayar kunnensa ,sautin muryar kukanta ya jiyo can kasa tamkar ta baby yana shiga cikin dodon kunnenshi, zuciyarsa ta cigaba da bugawar da take da karfin gaske, wani irin rad'ad'i ya dinga jin yana sauka akan tsokar dake makale da kirjinsa , runtse idanunsa yayi sosai had'e da Jan dogon tsaki sannan ya katse kiran gabadaya ya Mike ya shiga bathroom...

Muwaddat kuwa har lokacin tana zaune tana kukan bakinciki abinda bunayya yayi mata , kukan ma ba wai akaron kanta taso yinsa ba, ji tayi kawai hawaye na fita daga cikin kwarnin idanunta, tayiwa kanta alkwarin duk runtse babu abinda zai sake shiga tsakaninta dashi, idan mutuwa zatayi da soyayyarsa , sai dai sonsa ya kasheta ,amman babu ita babu shi har abada ko komawa tayi lagos bazata shiga tsabgarsa ba .
tana cikin wannan kukan mumy tashigo d'akin ganin har 11:00 na dare bata fito taci abinci ba .
Tana ganin shigowar mumy tasoma k'ok'arin had'iye kukanta had'e da share hawayenta da sauri ,yayinda ita kuma mumy tana ganin haka ta maida kofar da sauri ta rufe ta k'arasa shigowa d'akin tana kiran sunanta "muwaddat meke faruwa ?
" lafiyarki ?
"kukan me kike?
"Waye ya mutu ko waye bashi da lafiya ?
Tayi mata tambayar gabadaya ajere tana zama kusa daita.

kai kawai muwaddat tashiga girgiza mata al'amun babu komai "ke ki bud'e baki ki min magana, ba wai ki dinga karkad'awa mutane kai ba "me ya faru ,me yasameki ?

Muryata cike da kuka da in ina tace " ba..Babu komai fa" "babu komai zaki zauna kina kuka kamar wace aka aikowa sakon mutuwa, ki gaya min abinda ke damunki ?
Wasu sabbin hawayen suka sake gangaro wa bisa kuncinta , tasa bayan hannunta ta goge tana sake girgiza mata kai .
Hankalin mumy ya sake tashe matuka, tace "wato kina boye min Abu ko ?
Cikin rawar murya tace "Sam Sam ba haka bane mumy ,"kina boye min mana mumuy ta fad'i tana mai mikewa tsaye da sauri tayi hanyar fita domin kiran dady, muwaddat tayi saurin riko tafin hannuta "mumy karki yi fushi dani Dan Allah ,babu fa abinda ke damuna kawai dai ina cike da kewar ummina ne .....

ta tsinci kanta da fad'ar haka wasu siraren hawaye na gangaro mata .

Naunayen ajiyar zuciya mumy ta sauke sannan ta koma ta zauna tana dubanta had'e da nazarinta "har ga Allah ta yarda da maganar diyarta, saboda tasan yadda shakuwar dake tsakaninsu da uwarta tafi karfin haka ,domin kuwa daya baya iya d'aukan dogon lokaci batare daya ba ,yanzu haka kullun garin Allah ya waye akalla basuyi waya ba sai sun yi sau Goma hatta bacci suke tashinta wani lokacin ko abinci zata ci sai takirata tana cin suna waya haka zalika abi ,Yayinda komai akayi ta bangaren kowanensu ,yanxu ne zasu bugawa juna suna cike da tsantsar farinciki suna labartawa juna "
Ahankali mumy ta bud'e bakinta "to kuma shine zaki zauna kina kuka?
" idan kin gaji da zama damu kamata yayi kiyiwa umminki magana tasa azo a tafi dake .. .. ba wai ki zauna a d'aki kina kuka irin hk ba "
Amman yanzu ki bari zuwa wani sati sai ki koma, saboda ina son kije kalgo ki ga inna kafin ki koma, ki d'an yi kwana biyu agurinta ,dan koda yaushe idan munje sai tayi maganarki ,Dan haka zan saka ala'meen ya kaici gobe tunda weekend ce sai kiyi musu kwana biyu "zuwa lahadi ko manday sai ku dawo, ki soma shiri komawa
Muryarta a matukar raunane tace "to mumy "

Mumy tace "Muje ki ci abinci Sam baki son cin abinci muwaddat, shiyasa gashi nan kullun jikin naki babu laka bare kuzari ,muwaddat ta Mike tsaye jikinta a matukar sanyaye tayi gaba tasoma tafiya tamkar kazar da kwai ya fashewa aciki , mumy ta bi d'akin da kallo sannan ta kai hannunta Kan wayarta dake yashe Akan gadon ta d'auka tana duddubawa, babu abinda ta gani duk number's din yan gidansu ne Dana kawayenta , sai number guda daya data ga an rubuta (man) muwaddat...mumy ta kira sunanta. ...
ta D'an tsaya tare da juyowa ta tsaya tana duban mumy "waye kuma man ?
"Tayi shiru can tace " d'an makarantarmu ne "meye tsakaninki dashi ?
"Babu komai momy "to ki goge lambarsa bana bukatar ganinta cikin wayarki ,sannan ki dinga kiyayewa ,Allah kuma ya kiyaye mana ku a duk inda zaku sanya kafafunku .

Muryarta ahankali tace ameen ta amshi wayar ta goge number man har ma data Auwal gabad'aya sannan ta sake juyawa ta cigaba da tafiya mumy ta biyo bayanta ,
Mumy na fita ta kira ala'meen a waya ta sheida masa abinda take so ayi a gobe idan Allah yasa suna raye ta kirasa Dan ya kwana da shirinsa ,yace mata "babu damuwa Allah ya kaimu.
Tun daren al'ameen ya shirya kayansa set biyu kacal ya d'auka sai kayan Pajams dinsa haka ma muwaddat mumy ce ta shirya mata kayanta cikin yar k'aramar akwati ..

Washegari tunda sanyi safiya suka d'auki hanya zuwa kalgo, gudu kawai al'ameen yake sharara akan titi batare daya juyo ya kalli inda muwaddat take ba ,haka zalika itama bata kalli inda yake ba idanunta naga kallon titi ne, domin haushinsa take ji acikin zuciyarta, ganinta duk shine silar damuwarta silar da yasa ran bunayya ya 'baci har suka samu sa'bani dashi , Dan da kace bai aiko kiranta ba alokacin da duk hakan bata kasance ba ..
Tun yana dauriya har dai yasoma janta da hira tana amsa masa tana yatsina fuska amman ya

dakewa zuciyarsa ya cigaba da janta Dan dai ta saki ranta sannan yana bukatar tafiyar tayi masa dadi gashi ga rabin rayuwarsa ,tafiya ce mai nisa tsakanin ilorin da kalgo sannan suka iso ..
suna shigowa kauye ya rage gudu
Adaidai wani madaidaicin gida yayi parking din motarsa ya fito yana Mika had'e da salati ,kusan minti goma ta fito tana kallon yanayin garin ,yana nan dai tamkar yadda ta sani acan baya sai 'yan canje canje kad'an da taga garin ya samu na cigaba ,ciki kuwa har da gidan kakarta ,Kafin kace me tuni kofar gidan sun cika da kananun yaran unguwar da almajirai suna kallonsu had'e da zagaye motar .

Daya daga cikin yaran ya k'araso gurin ala'meen yana washe baki "yaya ala'meen sannu da zuwa "yauwa musa sannu ya kake ya gida ?
ala'meen ya fad'i hk yana zagayo ya bud'e boot ya d'auki akwatin kayanta,musa yayi sauri ya amsa had'e da shiga cikin gidan inna .
Ya waigo ya dubeta tana kallon yaran dake zagaye suna wasa da tsalle tsalle "Muje ko ,nasan kin gaji dayawa "ba tace masa komai ba ta nufi hanyar cikin gidan tun
daga farkon shigowarta gidan tasan ba iyayenta kad'ai rayuwa ta sauyawa ba har da kakarta , koina tsaf tsaf sannan a tsaftace malale da tayis har cikin tsakar gidan bakinta d'auke da sallama tasanyo kanta ta k'arasa shigowa, inna dake tsaye jiran shigowarta tun shigowar Musa ta fad'ad'a fuskarta da fara'a tana murnar ganin jikarta, "marhabun lale da mutanen iko da ilorin "muwaddat ta saki murmushi me tattare da gajiya sannan ta k'arasa ta rungume inna ajikinta "inna mun sameku lafiya ?
"Lafiya kalau ya hanya ?
Bata amsa ba ta saki inna tana dubanta "mu shiga daga ciki sannu kun kwaso gajiya "babban ango maraba sannu ,kun sha hanya "sai yanzu kika ganni tun dazu nake ta faman bud'e makoshi ina rattafa sallama amman kikayi min banza "yi hakuri mai gidan asaliyyan, ni na isa in shareka ai ko zan yi shariya sai dai in share wancan mai wuyan kamar lagwani , amman ba kai ba ,suka saka dariya ita dai muwaddat tayi gaba tashiga d'akin da inna ta nuna mata .

Tana shiga ta zauna gefen gado tana tunanin abinda zata fara yi sallah ko wanka cikin haka inna tashigo d'akin tana sake yi mata sannu ,muwaddat ta yatsina fuska "Sannu me kuma zaki min ni da ke wuya kamar lagwani ?
Inna tasa dariya jaira haushi kikaji kenan ?

"Dadi abun yayi min shiyasa "ke jaira banciki da bakin ranki ,yanzu dai dame zaki fara wanka ko sallah ko abinci ?
"Ina bayi tukunna dan gaskiya wanka zan fara ,
Inna ta nuna mata bayi sannan ta sake yin waje .
Muwaddat ta Mike tsaye ta bud'e akwatin kayanta ta ciro white towel ta d'auki makilin da brush ta nufi bayi wanka tayi ta fito ta sauya kaya zuwa doguwar riga sannan tashiga Jero sallolin dake kanta ..
Bayan ta idar ta kai idanunta Kan hadadden kafet din dake gabanta kwanunka abinci ne sama da Goma ajiye ta d'ago tana duban inna tamkar zatayi kuka "wadan nan abincin fa inna?

",duk ke akawowa ki bubbude kiga Wanda yayi miki ,kai ta girgiza sannan tace "wane kika dafa aciki ?
inna Ta janyo wata kula blue ta bud'e "ga Wanda na dafa miki "to shi kawai ma ya isa shima din kad'an zanci .

Inna ta Mike zata fita amman jin abinda ta fad'a yasa ta d'an tsaya "ki dibi abinci kici sosai sannan ta sanya kai ta fita muwaddat ta d'auki plet ta dibi abinci kad'an tasoma tsakura bayan tagama ta nemi guri ta kwanta akan gadon inna ta ciro wayarta ta kunna takira mumy ta sheida mata sun iso ,sannan takira iyayen goyonta, suka hira har sanda ala'meen yashigo wayar take ,Dan haka bai ce mata komai ba ya koma gurin inna .

****
Alameen Suna zaune tare da Inna suna Hira, cikin hirar ne take Masa zance aure" ala'meen yakamata zuwa yanzu ace ka'ajije iyali ga sa'anin haihuwarka Nan daga masu mata biyu sai uku sannan kowane da ya'yansa abun sha'awa, Mai zai Hana kai ma kasamu sukuni ka samu ka duba yarinyar data dace ko anan cikin dangi ne ka zaba ..?

Ala'meen Yayi murmushi kawai Yana duban Inna har sanda ta numfasa sannan yace "maganarki gaskiya ne Inna yakamata, sai dai har yanzu ina kan dubawa dai, inshallah Nan ba da dadewa ba zan kawo Miki kyakkwar kishiya wacce tafiki kyau da komai ..

Koma wace balarabiya ce fatana ka kawo ta gari yar gidan mutunci , ni kuwa sai naji ina maka sha'awar auren ayshatu ,wallahi baka ga yadda kuka dace da juna ba ,da zaka yarda da shawarata sai ka nemeta nasan babu abinda zai Hana ubanta yaki baka ,Kuma Nima zanyi farinciki sosai, Kai kowa ma zai ji Dadi hakan ta fad'a Tana duban ala'meen,ta ga yadda zai d'auki maganar .

 yadda take dubansa din yasa kirjinsa bugawa saboda maganar ta bugesa Sosai ,jin yayi shiru tace banji kace komai ba .?

"To me kike son nace Inna ?ni kaina abinda ke cikin Raina kenan ,amman gabadaya yarinyar taki bani damar fahimtar daita, zan dai Bata lokaci Nan da kafin ta koma zanyi kokarin sanar mata," to ka hanzarta Dan dai saboda Allah zuwa yanzu yadace ace ka'ajiye iyali ,idan Kuma kafinson na mutu Banga aurenka ba to shikena..
ya kamo hannuwanta duka cikin nasa Yana Bata fuska "Kai Inna karki fad'i haka ,da yarda Allah bama aurena ba hatta ya'yanmu nida akram sai kin gansu,
"kai rabani da zance wancan ja'irin tsohon tuzurun, koda yaushe shima hk nake fama dashi akan batun aure, har ma gara kai yanzu tunda nasan inda ka dosa, shi fa ko mgnr auren ma baya kauna yanzu, byn shekaru baya da kansa ya kawo min karar iyayensa akan yana son aure amman yanzu na rasa dalili , wasu abubuwa ma nagani nayi kmr wanda aljanna ta aura ..
"duk yarinyar da aka nuna masa sai yace batayi masa ba.
ala'meen ya numfasa kana yace "ni kaina abubuwan akram na damuna da ta'ba min zuciya, gabad'aya tun dawowarsa daga canada na rasa gane kansa da gindinsa , gashi yau ciwo gobe

lafiya, kwanaki dana yi masa rakiya ganin likita ,karkiji irin fad'an da likitoci sukayi masa akan wasa da rayuwarsa da yake ,wai zuciyarsa na daf da bugawa, tambayar duniya nayi masa amman amsa daya akram yake bani babu komai ,shi baya tunanin komai alhalin ni nasan akwai abinda ke damunsa boyewa kawai yake , dan wallahi inna kwana akram yake yana kuka da buge buge a d'aki shine ma dalilin dayasa na bar masa d'akin na koma sama.

"subuhanallah shikenan zargina ya tabbata, aljanna ce wallahi ta auresa, to ka sheidawa iyayensa ko ,dan asan matakin d'auka?
"a'a inna ni dai nakan yi masa addua alokacin muna tare ,aiko bamuga ta zama dole a nemo masa taimako..
Hira sukayi sosai har sai daya ga ala'mun inna ta fara jin bacci sannan ya bar gidan Yana mata sallama .

****
duk inda yakamata ala'meen ya Kai muwaddat ta sada zumuci ya kaita sai yan tsirarrun gidajen 'yan'uwa da gidan innarsa ne Bai Kai ba, suka barshi sai zuwa gobe lahadi Wanda daga Nan zasu wuce . .

Tun da safe ya kaita gidan munira ta amshe su cike da fara'a tare da nuna mata gurin zama da murnata da komai ta karbeta hannu biyu biyu duk da basu wani san juna ba sosai saboda tun Tana yarinya rabonsu da juna ,muwaddat taji Dadi sosai saboda ita dai mutun ce Mai son a nuna ana sonta ,Kuma adamu daita tare da rawar jiki akan lamarinta, suka gaisa a mutunce cikin haka Mai gidanta ya fito ,yana ganin ala'meen yace "babban Yaya kun iso lafiya tun jiya nasamu labarin zuwanku ya mutane can ?ya Mika Masa hannu suka gaisa ala'meen yace "kowa lafiya duk sunce agaisheku ..
cikin farar mijin munira yace "bakuwa sannu da zuwa ya hanya ?
Muwaddat ma tayi Dan yi murmushi kad'an Tana gaidashi ,munira kuwa sai rawar jiki take Tana Nan Nan da muwaddat kafin kace me ta cika mata gabanta da abinci ...

Muwaddat Bata wani ci abinci kirki ba har gara ma lemu ta kan Dan tsiyaya Ta sha .

Bayan awa daya ala'meen yace wa mijin munera "Dan Allah Bala idan bazaka damu ba ina son munira ta raka yarinyar nan gurin sauran dangi akwai inda bazan iya Kai ta ba ,gashi goggo tace" akaita Koina acikin dagin ta sada zumuci Bala yace" shikenan babu damuwa sai ta kaita ai "Yana gama fad'ar haka yayi gaba, shima ala'meen yace Bari ya Dan shiga gari kafin su dawo har ya Kai bakin kofa ya juyo Yana dubanta karki damu munira zata Kai ki duk inda yadace .

Gyada Masa Kai kawai tayi batare datayi Masa magana ba, munira tace Bari na shiga na shirya nazo mu fita ga mamakin munira sai ji tayi tace" kariki damu kanki ki Bari kawai ba sai munje koina ba ,Nan ma kawai ya Isa wallahi garin akwai Rana sosai" keda da aka kawoki a cikin mota koina ac "
Muwaddat tayi murmushi "bana son fita ne wallahi mu zauna muyi hirarmu har zuwa sanda zai

dawo , munira tayi sororo Tana kallonta sannan tace "Anya ayi haka bayan kinji abinda goggo tace .?

"Mubari kawai ai muje gurare dayawa jiya tashiga fad'a mata inda sukaje jiya dan haka muyi zamanmu muyi Hira ... ana suka wuni zir suna Hira sai wuraren la'asar ala'meen ya dawo munira tayi Masa sannu da zuwa tare da tashi ta kawo Masa ruwa Mai sanyi ,ya amsa ya Sha idanunsa na kan muwaddat ,ala'meen ne ya fara magana "yau dai kun Sha yawo .

Muwaddat tayi shiru domin ba tasan me zatace ba, sai munira ce tace "ai bamuje koina ba domin dai tace bazata iya bin Rana ba.
ala'meen ya tsira mata ido yana kallonta batare daya ce komai ba ,anan ya fahimci momy ce kawai ta damu datazo gurun danginta amman ita Sam Bata wani damu ba .
Tun shigowarsa muwaddat ta kasa sakewa bata wani Sanya baki cikin hirarsu ba saboda ala'meen dake binta da mayatacen kallo ,duk inda ta motsa idanunsa na kanta wanna dalilin yasa ta kasa sakin jikinta ..

Can bayan kmr minti goma ya dubeta "tashi muje ko Kar muyi later saboda Ina son na bita ta gidan hajiya batayi magana ba ta Mike ta d'auki Jakarta ta rataya tayi gaba .
munira ta mike tayi musu rakiya har harabar gidan inda ala'meen yayi parking din motarsa .

Ala'meen yashiga mazaunin direba itama tashiga ya tayar suka tafi har suka shiga wata unguwa, taga yayi parking din motarsa a wani kofar gida ya d'an dubeta Dan Allah kiyi hakuri zamu shiga wurin hajiya mu gaisa .

Batare data juyo ba tace "shiga ka fito ina jiranka ,bai ji dadin yadda tayi Masa ba, koda yake me yiwuwa dan batasan wace hajiyar yake nufi ba ,amman ko batasani ba sai ta tambayeshi ,shi Kuma sai ya fad'a mata gidan hajiyarsa yake nufi yasa Kai ya fita Tana kallonsa ..
har zai shiga gidan sai Kuma ya dawo ya tsaya ta bangaren da take '"ki fito mu shiga Dan Allah gidan yayan mumy ne fa da suke ciki daya, wato mahaifina kinsa mumy bazata ji Dadi kixo garin nan har ki tafi baki zo kun gaisa ba ,jin haka yasa ta fito Tana yatsina fuska tamkar wace taga Kashi .
Tasoma tafiya ahankali har suka shiga cikin gidan .

Jin kad'an ta fito ta shiga motar tayi zamanta .. Koda ya fito yasameta cikin motar Tana waya bai yi mata magana ba ya bud'e motar yashiga ya tayar .

Yana sauketa agidan inna ya k'ara gaba ,domin ya tsani yadda take yi Masa ,a yadda ya lura shi kawai takewa wannann miskilacin amman ai Yana ganin yadda takewa mutane ko d'azu daya koma gidan munira d'aukota Hira ya iskesu suna yi har da dariyata amman Tana ganinsa tayi shiru Bata sake cewa komai ba .

Da sallama tashigo gidan Tana yatsina fuska Inna ta dubeta Tana yi mata sannu "kin gaji ko

Daman ziyara haka yake dole ki gaji baki saba ba "wallahi Inna duk na gaji garin nan naku akwai Rana "Inna tayi murmushi in go nan tayi mata dakuwa ,"Allah yasa dai kema garin naku ne Kuma inshallau acikin garin Zaki karasa rayuwarki "Kai Inna ina zan iya rayuwa anan ,ku dai daya zamemu ku dole kuyita fama, mu ma dinga zuwan muku ziyara ta k'arasa maganar Tana shigewa d'aki dayake Bata fahimci inda zance Inna ya nufa ba ....

Daddare ala'meen yashigo gidan yasa mu Inna Tana zaune akan tabarma yayinda muwaddat ke kwance akan gadon Tana rike da waya da dukkanin alamun chatting take, bayan sun gaisa da Inna ya waigo inda take kwance ya Kira sunanta..muwaddat

Ta yatsina fuska sannan tace na'am '"ki shirya gobe da wuri saboda fitar asuba zamuyi "to kawai tace Masa atakaice Tana juya Masa baya ..

Inna tayi kasa da muryarta can ta yadda muwaddat bazata jiyota ba "wai yana ga Kamar kana jin tsoron yarinyar, ka fad'a mata abinda ke ranka mana Kar fa wani yayi maka shigar sauri, duk da dai tunda tazo Banga Wanda ya kirata ba, ko ita takira ba ,bayan iyayenta "girgiza Kai yayi "ba yanzu ba tukunan Inna "
"ya dai tabbata dai tsoron nata kake ji?
"to kusan haka ne Inna duk lokacin Dana yunkuro zan fad'a mata sai fargaba ta hanani .."ina ganinka jarumi a she kaima lusarina ne bansani ba.... "yanzu meye abun fargaba da jin rsoro anan?
" to Bari ni na sanar da iyayen nata "a'a Inna karki yi sauri yanke hukunci haka ,kinsa fa gaugawa daga sheidan ne, ki Bari mubi komai ahankali ke dai kiyi min addua kawai "to shikenan Allah yasa rabonka ce ,yace "ammen suka shiga wata hira har sanda goma ta buga yayi mata sallama da zai wuce ya k'arasa inda take kwance idanunta a lumshe suke ala'mun tayi bacci ya Dade tsaye akanta Yana dubanta Yana jin sanyi aransa sannan daga baya yasa Kai ya fice ....

****
Washegari tun safe suka d'auki hanyar komawa ilori d'auke da tsaraba kauye iri iri danginsu daddawa kuka da gasashen kifi sai Kuma dankalin hausa Wanda yazamoto abinda aka fi nomawa kenan agarin kalgo ....
Agajiye suka k'araso ilori saboda mugun gudun dayayi akan titi ....
Suna shigowa harabar gidan idanunta ya sauka akan muhammed auwal zaune akan motarsa Yana fuskantar kofar tafkeken get din gidan yana ganinsu tare cikin motar yayi wata irin zabura ya duro ya tsaya yana kallon motar zuciyarsa na wani irin mahaukacin bugu.

Ta tsura masa ido har sanda ya tsaya jikin motarsa ya harde hannayensa duka a saman kirjinsa tamkar wani babban mutun ,ahankali ta cigaba kallonsa kirjinta na wani irin mahaukacin bugu lokaci daya hankalinta yayi mugu mugun tashi ,kallo daya zaka mata kasan cewar ba cikin natsuwarta take ba ,tana cikin zallar tsoro da abinda idanunta suka ci karo dashi ne, sam batayi tunanin ganinsa a daidai wannan lokacin ba, ba ita ba hatta ala'meen ya d'an samu buguwar zuciya da irin kallon kaskanci dayake aiko musu dashi .

Gaban bunayya ya dinga faduwa ya kura mata tsumammun idanunsa yana kallonta sam ya kasa d'auke idanunsa akanta yana duban abun tamkar a mafarki ,yayi bala'in mamakin ganinta tare da ala'meen, ya fara taku ahankali zai zo gurinta sai kuma wata zuciyar ta gargadeshi akan gara dai ya cigaba da tsayuwarsa a inda yake zai fi masa alkhairi ,idan ma ya k'arasa inda yake yace mata me ?

Dan haka ya koma da baya ya jingina bayansa da jikin motarsa ya cigaba da kallonta ,Kallonsa take yi itama cike da matsanancin tsoro sannan a matukar kidime tun daga kasa har sama kirjinta na bugawa, zuciyarta kuwa kamar zata fito daga cikin kirjinta .
Gabadaya halitar jikinta babu inda bai amsa ba .
Da kyar tasamu ta yunkura ta zata fito daga cikin motar dan tuni ala'meen yayi parking taji sautin muryarsa a kasalance "koma ki zauna tukunna.....

Mmn sudais ce
2/4/20, 8:39 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

alhamdullahi am back again.

warning!!!

for the first time !!!! i will like to say," don't read this novel if you know you are not married...

❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....wannan shine.

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

page 16

..tsaye yake acikin lanbun shakatawa na cikin gidan hannuwansa duka rungume a saman kirjinsa yana tafiya ahankali ahankali yana lumshe tsumammun idanunsa saboda sanyayyiyar iskar dake ratsa jikinsa ..
  kmr ance ya bud'e idanunsa kawai yaga faiza tsaye a gabansa tana fuskantarsa cikin mayunwacin halin da shi kansa bazai iya misaltawa ba,
ya d'an tsura mata ido yana Kare mata kallo na wani lokaci , sam itama bata da munin da zai kita, sai dai shi sam baya jin sonta acikin zuciyarsa, dan matukar muwaddah na rayuwa a doron kasa ba zai iya rabar wata mace da sunan soyayya ba, bare aure,tsawon minti goma suna haka sannan ya juya ahankali ya soma d'aga zara zaran yatsun kafafunsa cikin isa da izza ,tabiyo bayansa da sauri tana kiran sunansa yaya bunayya! yaya bunayya !!"dan Allah ka tsaya ka saurareni bakasan yadda nake jin zuciyata ba akanka.
 ko tsayawa bai yi ba bare ya nuna alamun amsawa kuma tabbass tasan yana jinta tayi saurin tarar gabansa tana ware masa hannuwanta duka "wai yaya bunayya me yasa kake min haka ne?
"me yasa kullun kake tsanata kiyayya gareni?
"ina da komai da za'a so mace dan shi ,to me yasa ni bazaka soni ba? tsayawa yayi kawai yana kallonta tmkr bai santa ba bare wata danganta dake tsakaninsu illa dogon tsakin daya jaja da karfi yabi gefenta ya wuce tayi saurin riko laulausar tafin hannunsa cikin karfin hali wanda hkn datayi yasa har taji wani azababben ciwon kai ...

cikin wani irin tashin hankali ya daka mata tsawa "kina hauka ne da zaki rike min hannu?"ko kin fara shaye shaye ne bansani ba ?
cike da kuzari da karfin zuciya tace " an rike maka hannu me zakayi?
" muhammed auwal bari na gaya maka lokaci yayi da tsawarka ta daina firgitani ,lokaci yayi da kowa dake cikin danginmu zasu san abinda ke tsakanimu da kai .....
tasss tasss taji ya saukar mata wasu gigitattun maruka har guda biyu akan fuskarta "ki kyaleni faiza ...ki rabu dani faiza, tunda nace ki kyaleni ,ki kyaleni mana ko ana so dole ne?
in soyayya ce nace bana yi ana so dole ne?
bari kiji daga yau karki sake takura min akan wannan shirmen saboda bana sonki bana sonki ba kuma zan ta'ba sonki ba ..yana gama fad'ar hk ya juya fuuuuuuu a fusace ya kalleta anan .

 tabi bayanshi da kallo fuskarta cike da tsansar damuwa da nadamar rike masa hannu datayi

watakilla da bai kai hannunsa jikinta da sunan mari ba, hawayen dake boye acikin kwarnin idanunta suka samu nasarar gangarowa bisa kuncinta, tasa hannu ta goge wasu na sake zubowa cike da matsanancin sanyi jiki ta bi hanyar baya dan kar wani ya ganta cikin damuwa ,most especial aunty'nta muwaddah wacce kwata kwata bata kaunar ta ganta cikin damuwa, koda faiza ta shiga d'akinta sai ta rushe da wani tsumammen kuka ,kwantanta damuwar data shiga baya fad'uwa duk yadda take tunanin M. A ya wuce nan,, ya wuce da tunaninta sam ba itace agabansa ba, "to ita yanzu ya zatayi da rayuwarta.. ?
"hakika bata san yadda rayuwarta zata kasance nan gaba ba matukar M. A yaki amincewa da soyayyarta ,"shin me yasa bazai sota ba ya rabu da aunty'nta tunda itace daidai shi ba muwaddah ba?
har yammanci rana tana kwance a d'akinta taki fito dan batason kowa yasan halin datake ciki ..

zaman M. A a gidan yasa faiza ta nemi takurawa rayuwarsa ,dan kuwa baya samun damar ke'bewa da sanyi idanunsa yadda yake so, duk abinda yake idanunta na kansa ,dan hk a daren ranar daya cika sati biyu da zuwansa ,ya kudurci a niyyar komawa lagos a washegari , lokacin da yake sanarwa dady zance komawarsa tana gurin, aiko taji haushi maganarsa, taji tmkr ta d'aura hannuwanta duka bisa kanta ta rusa ihu ne dan bakinciki tunda tasan saboda ita yasa zai koma.. ranar dai bata samu ishashen baccin kirki ba sbd tsananin tunanin M. A.
tun da garin Allah ya waye yasa awanke masa motarsa .
yayinda shi kuma yana can makale da muwaddah yana romacing dinta da sunan sallama ,yaso kwarai su koma tare ,amman taki sai daya gama tsotse mata baki da laguda mata jiki zuwa kirjinta sannan ya barta ya d'auki hanyar birnin iko..

da daddare suna zaune su duka a parlour'n dady ban da faiza dake kwance a d'aki cikin bargo tana fama da zazzabin tafiyar M. A ,ana cikin hira ala'meen ya shigo gayar da dady Wanda kaida ne kullun daren duniya zai shigo gurin dady su gaisa kmr yadda yaga yaya akram nayi, ihsan tace" yaya ala'meen d'azu na hau samanka ban sameka ba ,nayi zaton ko zance ka tafi gurin latifa ya cilla mata muguwar harara "to idan can naje sai me kin ganki ko mumy ... ,wallahi da ba dan ke din mai sunan mahaifiya bace dana shuka miki rashin mutunci yau..
Suka kwashe da dariya "ai kuwa da munganku arana inji cewar eiman ...

ihsan tace "bama za'a ganmu arana ba ,daman sako zan bayar ka kai mata,"sai ki bari idan zani ,eiman tace yaya ni kuma ina son zuwa gurinta ta min lalle da kitso , ala'meen yace "Allah idan kuka dameni da zancen wata latifa zan mazgeku yanxu, kun ji min yara da tonon silili kowa sai yasan da wata latifa..

suka sake kwashewa da wata dariya har dady ,wanda cikin dariyar yace ",ku rabu dashi zan sa direba ya kaiku sai kuje har muwaddat itama ta gano gari ala'meen ya dubi inda take zaune tana waya ,magana take kasa kasa a waya Amman babu mai jin abinda take fad'i ,saboda a hankali take magana ya tsura mata idanunsa yana kallonta yana magana da kannenta, kallo daya tayi masa ta d'auke kanta tare da gaisheshi ",ina yini maimakon ya amsa gaisuwarta sai yace ya zaman bakunta ?"lfy tace akaitace bai sake cewa komai ba ya samu guri ya zauna

yacigaba da kallonta .

M. A datake waya dashi yace "Halan wannan tsohon mayen ne ?"nifa Allah zan masa rashin mutunci akanki dan me zai dinga shiga tsabgarki, kema har da wani gaishe shi ya k'arasa fad'ar mgnr yana Jan tsaki"cool dawn kanina babu komai fa atsakaninmu, ka cire zargi zuciyarka "karka manta shi da kai duk abu guda ne agurina kmr yadda zan mutuntaka haka yazama dole na mutuntashi sannan na girmama shi ...
"tsaki ya ja " ki shirya next week zanzo in tafi dake sannan ya kashe kiran ..
Tayi shiru ta d'ago idanunta ahankali suka had'a ido da ala'meen yayi sauri kawar da fuskarsa gefe yana cigaba da hirarsa "hanyar d'akin ta nufa kar dai zargin Auwal ya tabbata al'amen sonta yake ?

"kai impossible hakan ma bazai ta'ba yiwuwa ba ,shi da yake da matar da zai aura ..shi kuwa al'ameen binta yayi da wani shu'umin kallo zuciyarsa na sake bun kasa da soyayyarta da tayi masa kamun kazar kuka .

Washegari da safe bayan an gama kalaci duk yaran gidan suna parlour'n mumy ,dady ya shigo gabad'aya yaran suka kaceme da hayaniya, kowa da abinda yake fad'i muwaddat ce kawai tayi shiru ta kama kanta saboda tun jiya da M. A yayi fushi daita akan yaya ala'meen ta rasa samun kwanciyar hankali da natsuwar zuciya dady ya dubeta yace "muwaddat ki shirya direba ya kaiki yawo ki d'an ga gari eiman tayi saurin cewa "Amman dady har damu ko? Dady yace da dai kun bari an kaita ita kad'ai idan kuka fita tare zaku dameta da hayaniya" kai dady yau fa week ce babu makarata kabarmu mu fita tare itama zatafi jin dadi ko aunty ?
Kafin muwaddat ta bata amsa dady yace "ko babu makaranta malamin lesson dinku zaizo an jima ..

Ana cikin haka sai ga ala'meen yashigo a shirye cikin shirin fita ,t shirt ce ajikinsa da bakin wando jeans, dady yace" yauwa tunda yayanku yau yana gida bama sai na had'a muwaddat da direba ba ,ala'meen ga kanwarka nan ka d'an fita daita taga gari, Dan tun zuwanta ba inda taje .

Ala'meen yayi shiru yana kallonta soyayarta na sake huda zuciyarsa, yana da inda zashi Amman hakan bazai hanashi bawa wannan fitar mahimmanci ba ,
Cikin rawar jiki yace ,"to dady ta shirya mana ai sai mu fita ya kalli eiman " fushin me kike yi ?

ihsan tace "wai Dan dady yace ba damu za'a je ba saboda lesson din zaa yi mana , alameen ya harari eiman "ai ko babu lesson bazaki shigar min mota ba sai dai ku fita direba ..

Dady yayi murmushi" wai me ke had'aka da eiman ne sam kafi biyewa faiza da ihsan akanta?
"dady yarinyar ce bata da kunya "eiman tayi saurin cewa "wai dady Dan akan aunty Ltifa tayi min waya ta tambayeni yana gida shikenan tun lokacin ya tsaneni ,dady yace to kai meye abun

jin haushi ba kai da kanka ka nuna kana sonta ba nima fa na lura a yan kwanakin baka zuwa gurinta kmr da ala'meen ya shafa sumar kansa yana murmushi "babu komai dady kawai ina hutawa zata janyo azo a dameni bayan nayi mata gargadi ko abokaina suka zo nemana karta kuskura tace ina gida sai dai idan ta tambayeni amman dayake mara jin magana ce da an xo nemana sai tace ina gida dady yace "ke eiman kinji abinda kikayi daga yanzu in ana nemansa kice yayi balaguro eiman tace "to dady ai shine yake cewa idan mutane sunzo nemansa su tambayeni kuma haka kawai sai na dinga yi karya,byn karya babu kyau ala'meen cikin wasa yace"zaki rufewa mutane baki ko sai na bubbugeki ,tayi shiru tana gunguni ya d'an waiga bai ga muwaddat yace "wai ina wace zan fita daita ne ?

Faiza tace bari na dubota tana ciki tana shiryawa tana shiga d'akin ta iske muwaddat kwance a d'akinta mamaki yakamata tace ",kai aunty ke da ake jira za ki fita yawo tare da yaya ala'meen shine kawai zaki zo ki kwanta .

Muwaddat ta d'an yatsina fuska ",nifa wallahi banason fita haka kawai ,ni bancewa dady ina son ganin gari ba A6mman dan rigima wai wani sai an kaini yawo "ko dai da yaya ala'meen ne baki son fita ?
"amman ina laifin a fita dake kiga gari tunda har yanzu bakigama sanin garin ilori ba ..

"Ke nifa ban iya fita da wannan magananne mutumin wallahi sai yasa Kan mutu ya d8auki caji Sam Sam maganarsa bata da limit "ke ina ruwanki da maganarsa ,tunda ke ba mai magana bace bare kice maganarsa ta dameki?
"Kuma ba surutu garesa ba ,wallahi idan kikaji yadda a waje ake complain din rashin kula mutane da bai yi sai kinyi mamaki agida kam ya kan 'bata lokacinsa akanmu, kuma yanzu kinga fita nashi uzurin zai yi dady ya sashi"
"Kin fahimcesa ba daidai ba shiyasa naga kin sauya fuska lokacin da dady yace ya fita dake yawo ..

"Kinga faiza banson dogon turanci kema yanzu na kula zama dashi yasa kin dawo aku kuturu , abinda za'a yi yanzu kawai kije kice kaina ke ciwo shiyasa nashigo na kwanta .

"Gasky aunty bazan iya ba kawai ki taso idan kika ki kmr kin wulakanta dady ne muwaddat ta yarda da shawarar kanwarta ta tashi ,ta sauya kaya jikinta ta shirya tsaf ta fito cikin wani had'adden material mai maseefar tsada kayan sunyi mugun kama jikinta tayi kyau sosai kana kallonta kasan yar Hutu ce ba'a kashe kudi a banza ba hatta jaka da takalmi kace domin kayan aka kerasu ta d'an yafa Gyalenta ,kana ta fito parlour'n dady ya dubeta yana driya "kai yar gidan daddy wannan irin kwaliyar haka kar fa ki gigita mutane gari gashi babanki bai tashi miki aure ba .
Ta dan yi murmushi saboda wasan da dady yake mata ala'meen kuwa idanunsa kyam akanta yana son yaga yadda zatayi magana zata ce mishi su fita ko kuwa Jan aji ba zai bari tayi mishi magana ba ,koda yake ta cancaci fiyye da hakan yacigaba da kallonta saboda kwaliyarta ta burgeshi, shiyasa sam ya kasa d'auke idanunsa akanta ,lokuta dayawa mace mai yanga tana

burgeshi amman baya son Jan aji yayi yawa kuma bai fiyye shiri da shagababbiya ba ,yana daya daga cikin abinda yasa yake gwasale eiman shagwabatar tayi yawa kmr itace auta idan tana wasu abubuwan ko sabir k'aramin kaninsu baya abinda take yi .
tun muwaddat na yarinya yasanta da shagwa'ba saboda gata da yayi mata yawa ,Yasan dole ne ta zama sangartacciya domin gata mugun abu ne kuma gata guba ne agurin wasu ya'ya Dan bakowanne Dan gata yake samun ingantacciyar tarbiya ba ,tun sanin dayayiwa muwaddat tana yarinya har yau da wannan fuskar yake kallonta ,shi yasa lokaci datazo yayi kmr bai Santa ba domin bayason yashiga harkokinta bare yasha haushi, amman d'an zaman datayi yanzu a gidan ya kula kmr tana da kamun kai ,domin yanayin halayenta suna burgeshi bata da son hayaniya kuma bata da yawon surutu sannan akwai natsuwa ,illarta girman kai da Jan aji, gashi shi yanzu zuciyarsa ta kamu da matsanancin soyayyarta....

Muwaddat tayi zamanta da Jakarta a hannunta shi kuma yaki yace mata tashi su tafi, sai dady yace "ku tafi mana tunda kin shirya ,zaman me Kuke?

Ala'meen ne ya fara mikewa batare idanunsa na akanta ba yace "ki sameni a mota bata amsa ba ta Mike tabi bayansa ,Kafin ta k'arasa gindin mota shi har yashiga ya zauna ,tasa hannu jikin motar tana kokarin budewa sai taji shi gam a kulle , bazata iya ce masa ya bud'e Mata ba ,kawai sai ta matsa ta bud'e gidan baya ta shiga ta zauna ala'meen ya d'an waigo kawai ya kalleta baice komai ba ,yayi zaton ko ta kasa bud'e gidan gaba zatace a bud'e mata ,Amman sai yaga ta kame a gidan baya ,a zuciyarsa yace lallai ma wannan yarinyar direba zata maidani ko me?

Ya dai daure ya tada motar suka tafi suna hawa titi ya fara sharara gudu ban da kidan zamani ba abinda ke tashi acikin motar ,glass din motar ya saita gefenta domin yasamu damar kallonta adaidai wannan lokacin wayarta tayi k'ara ta d'auka tana magana da abi Sai wani magana take cikin shagwa'ba.

Alameen ya natsu sosai ahankali take magana Amman ya fahimci da Wanda take waya ,har wani lallaminta t
yake "haba yar gidan dady menene abun fushi kuma ?
"Cikin zumbura baki tace "to abi bayan kaine yau baka tasheni a bacci ba shiyasa har na makara banyi sallah da wuri ba yace "kiyi hakuri abinda yasa tun asuba Dana shiga massalaci ban fito ba sai da gari ya waye sosai shiyasa ban bugo na tasheki daga bacci ba, na yi zaton idan umminki ta tashi zata tasheki Amman kibari in Allah ya yarda zan cigaba da tashinki da asuba ince dai idan na ta dake kiyi sallah kina min addua kullun ?

A marairace tace " haba abi ina maka mana taya daman za'ayi in yi sallah ban wa babana addua ba "yauwa yar diyata nasan zaki min ina fatan kina jin dadin zaman ilorin?
"Abi babu laifi garin akwai dadi "da fatan hajara bata takura miki don nasanta da zafi akan yaro "dady wannan karon bata matsa min ba da yake tasan halinka Dana ummi "to fatan dai baki da damuwar komai "wallahi abi babu wata damuwa,sai dai gaskiya ni abi ina son na dawo "ki k'ara

zama tukunna har yanzu da sauran lokaci kafin ki koma makarata ki dai dinga duba litattafanki saboda kinsa da kun koma zango karshe zaki shiga kuma zamanki anan zaki fi samun nasuwa saboda takurawar bunayya .

"Shikenan abi tunda kace haka na amince zan zauna Amman nayi kewarku ban da bunayya ,abi yayi murmushi "mu ma muyi kewarki ,bunayya daman wani kewarsa kikayi bayan kuna tare duk kwanakin nan ince yau kwanansa uku da dawowa, nan da sati biyu masu zuwa zai koma London take gabanta ya fad'i yashiga dukan uku suna hira da abi cikin nishadi shi kuwa ala'meen tukinsa yake Amman hankalinsa na gurinta sai lokacin ya gano yawon amsa wayoyinta datake yi ashe ba wayoyin samari bane da iyayenta take ko da wancan miskililin yaron da baya ganin mutunci mutane shi Sam yaron baya burgeshi ..
Satar kallonta yacigaba dayi wato Dan tsananin gata har tashinta suke daga bacci ,bayan daren da suke rabawa suna waya ita dasu .

Bai rage gudu ba sai da suka shiga ciki wata unguwa sannan ya rage gudu ya karya kwana yashiga cikin layin a kofar wani madaidacin gida yayi parking ya bud'e murfin mota ya fito ya Dan jira ko zai ga ta fito daga cikin motar Amman sai ya lura bata da niyyar fitowa wata wayar ma take amsawa sai ya tuna ashe bai gaya mata cikin gidan zasu shiga ba ,sai daya bari tagama wayar sannan ya bud'e mata murfin motar "bisimillah ki fito muje ki gaida matar abokina ya tsira mata idanu ko zatace wani abu batayi magana ba ta zuro kafafunta ta fito daga cikin motar suka jira suka shiga cikin gidan .

minal ce ta fara tararsu da faraa ta kaisu parlour'n ta tana fad'in "kai alameen sai yanzu tun dazu ake jiranka Amman ka shanya min miji ,yayita kokarin nemanka a waya bai sameka ba .

"Al'amen yace ku ya femin madam wallahi wani Dan uzuri ne ya tsaidani, ya fad'a yayinda yake kokarin zama a daya daga cikin kujerun kushin din parlour'n ya d'an dubi muwaddat sannan ya cewa minal "madam gafa bakuwa na kawo miki .

Itama ta dubi muwaddat cike da faraa yayinda ta nuna mata wurin zama da murnarta da komai ta karbeta sai kace tasanta muwaddat taji dadi sosai da irin tarbar da minal din tayi mata ,suka gaisa a mutunce ta fara tsokanar al'ameen in ce sabon kamu akayi shiyasa tutar latifa ta fara dusashewa ?

Cikin murmushi yace "no wannan kanwatace a lagos take ta d'an zo mana Hutu ne ina angon naki ?
"Yana ciki gajiya yayi da jiranka shiyasa ya shiga ya Dan kwanta bari na tasoshi .

Tana shirin shiga sai gashi ya fito daga bedroom dinsu ganin ala'meen tare da muwaddat ya sashi washe Baki da yake ya taba ganinta sau biyu dayaje gidansu cikin fara'a yace "a she ba kai kad'ai bane ,cewa zakayi yau muna da babbar bakuwa ya fad'a yana kallon muwaddat.

Ta dan kirkiro murmushi dole kana ta gaida shi minal kuwa sai rawar jiki take tana nan nan da muwaddat kafin kace me duk ta zagayesu da abubuwan motsa baki al'maen Yasan ba lallai bane muwaddat taci abubuwan da aka kawo mata Dan haka yayi hanzarin cika cup da ruwan lemu ya tura mata gabanta ,abun mamaki sai yaga ta d'auka tasha suna ta hira minal sai tsoma muwaddat take cikin maganar dole sai da muwaddat ta saki jiki tashiga cikin hirar ,ta dinga saka baki jifa jifa, ala'meen zuba mata ido yayi saboda lura dayayi yadda yarinya ta iya lafazin iya magana cikin natsuwa tare da kwantar da murya da gogewar harshe hakan ya tabbatar mishi da tasan abinda take ,ala'meen ya dubi minal sannan yace "madan Dan Allah zan barta anan saboda inda zamu da oganki idan mun dawo zan kaita taga gari kmr yadda dady ya bukata minal tace "babu damuwa ya Mike ya kada mukullin motar dake rike a hannunsa tare da watsa idanunsa akan muwaddat Amman ita Sam bata kallesa ba asalima hankinta na can gurin turawa M. A sako .
Yace "ayshatul muwaddat ki zauna anan kafin muje mu dawo muryarsa ta ratsa cikin dodon kunnenta da sauri ta d'ago kanta suka had'a ido saboda yadda yakira complete name dinta ya razana zuciyarta domin tun tasowarta babu Wanda ke kiranta da wannan sunan bayan Auwal dinta sai yanzu dayayi mata ,da muwaddat akasanta kuma dashi kowa ke kiranta, ita kanta mantawa take da sunanta na gasky saboda ba'a kiranta dashi sakamakon sunan uwarsu ummi ne daita, suna girmama sunan babu abinda yabata mamaki kmr yadda ala'meen yayi amfani da sunan gurin kiranta ..

Ahankali ta gyada masa kai kawai Amman batayi masa magana ba, har ya fice daga parlour'n suna hira da minal saki fuska da fara'ar da minal ta nuna mata ya burgeta da kuma kyakkyawan tarba da rawan jikin datayi daita yasa taji tana son minal .

Minal dai yar wani fitaccen d'an siyasa ne anan garin ilorin ba'a Jima da yin bukinsu da Hisham ba Wanda ya kasance babban aboki agurin ala'meen tare suka kare karatu a Rasha har yanzu minal karatu take ,ayanzu haka tana karatunta a jamiar ilorin, hira ce ta balle tsakanin muwaddat da minal tamkar sun dade da sanin juna muwaddat ta saki jiki sosai har kowa ya labartawa kowa tarihin rayuwarsa.

Anan muwaddat ta wuni cur a gidan minal sai kusan yamma sannan ala'meen suka dawo daga unguwar da suka tafi suna cikin mota akan hanyarsu ta dawowa ala'meen yace bari in kira yarinyar nan ince mata gamu nan zuwa zan d'an zaga daita yawo sai mu koma gida .

Har ya fiddo wayarsa da niyyar zai kirata sai kuma ya tuna bashi da number ta ,yayi tsaki ya maida wayar aljihunnsa hisham ya dube sa yace "Anya manage babu wani abu tsakaninka da yarinyar nan?
Ala'meen ya Dan hararesa yace ",me kagani ?

"Ni Kan haka nan naji zuciyata na zargin akwai wani abu koma ince akwai soyayya mai karfi tsakaninku "kai rufa min asiri ai wannan ba irin tamu bace "saboda me kace haka ala'meen byn akwai zumunci mai karfi tsakaninmu ?
"nasan babu yadda za'a yi ka furtawa iyayenta kana sonta suki baka ,sannan ka daina ganin tafi larfinka..

Ajiyar zuciya ya sauke da karfin gaske "duk ba haka bane yarinyar ce yar shagwa'ba kai kanka kasan bana shiri da yan shagwa'ba ya fad'i hk yana waskewa ,zuciyarsa na dokawa ,domin a yanzu ma dayake maganarta wasu wurare a kirjinsa sake bud'ewa sukayi soyayyarta na kara nikaya aciki .

Hisham yace "Amman ni kuwa yarinyar batayi min kalar shagwababbiya ba..
"Eh to wani lokacin ni kaina ina mamakin yadda take magana a natse Amman shagababbiya ce gurin daka ganta ,iyayen goyonta sun sangartata ainun kar mutun yaje yasaka kansa cikin tasko."ai kuma ba daga nan take ba bakowa gata yake lalatawa ba ,akwai wasu ya'yan gatan da zaka gansu da tarbiya da kamun kai idan dai kana sonta na bada goyon baya dari bisa dari Dan gaskiya yarinyar tayi da kace aurena bai Jima ba Dana k'ara ta biyu daita idan kai baka da ra'ayinta ..

"Dan iska to yaya zakayi da minal ?
"Yaya kuwa zanyi daita Karka fa manta nmj nake inda daidai da auren mata hudu "to kuma duk Dubin matan dake garin nan basu yi maka ba sai bakuwar gidanmu ,hisham cikin dariya yace" ita naga ta min kasan nafi son auren yayan Hutu shiyasa nake sha'awar in tara matan Hutu agidana nayi ta hutawa dasu "to kuwa kwalelenka anan ,wannan tafi karfinka "ta yaya kake tunanin tafi karfina? Ince abun ba kokuwa bane ya k'arasa mgnr yana kwashewa da dariya " alameen yace "ka hakura kawai Dan ba baka zamuyi ba "idan Baku bani ita ba zaku jikata ku sha ne ?
"No no saurayi dai zamu bawa danye sharab Wanda ba'a cirewa yanar kaciya ba domin yarinyar bata dace da auren nmj mai mata ba "

Hisham yayita dariya har da rike ciki "kai nafa San inda zamceka ya dosa Amman kake son yin wani kwana kwana kai kace min hasashena gaskiya ne ...
Wallahi duk wani kauksucenka Nasan kana son yarinyar nan so kuma mai girma ,tun zuwana gidan na nasan za'a rina, a duk ruwan idonka da wuya ace baka sota ba ,ba zanga laifinka ba domin kuwa yarinyar akwai ruwan kyau Amman karka manta kmr a kunnen latifa domin ni zan fara bata labari za'a yi yar gida cikin murmushi alameen yace "sai kabari dai sai na fad'a da bakina sai kaje ka sanar mata dayake mamatace "to meye maraban dambe da fad'a ?
Alamen yace" zage zage sukayi dariya hisham yace "tunda uwar lafita ta rigada tace Tabaka ai tamkar tazama matarka ce fatiha ce kawai da za'a shafa ba .
Alameen yace " kai ni rabani da zanceta ba ita nakeyi ba yanzu " sai ta muwaddat ba ,ai nasan za'a rina tunda kai ba mutumin kirki bane.."ni wallahi tausayi yarinyar take bani itama hjy mantawa tayi da halinka shiyasa ta nanika maka yarinyar ..

Suna ta hira har suka iso gidan suna shiga parlour'n suka iskesu suna hira ,muwaddat kishigid'e Akan kujera kanta ko d'ankwali babu ana iya karewa dogon gashinta kallo Wanda ya sha gyara yagaji ,sai kyalli yake,da alamar hirar tayi mata dadi domin hankalinta baya kan komai sai tautaunawar da suke ita da minal Dan haka bata lura da shigowarsu ba sai da hisham yayi magana tana waigowa taga duk ita suke kallo ..

Mmn sudais ce
2/4/20, 8:39 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

warning!!!

don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

page 19

....yana jin ta kashe wayar gabad'aya ,ya zame ahankali ya kwanata dafe da marasa dake masa zugin sha'awa ,cikin wani irin shauki yasoma juyi akan katifarsa tare da runtse tsumammun idanunsa da suka gama canza kala tsabar jarabar dake cinsa.

kusan awa daya ya d'auka kwance batare da bacci yayi nasarar d'aukarsa ba, illa juyi daya keta faman yi rike da mara, da kyar yasamu ya yunkura ya sauko daga kan bed yashiga bathroom yayi wanka ya fito ya sake kwantawa yana rawar sanyi ,dan jin yayi tmkr wanka da yayi ma sake k'ara masa wani sabon sha'awa yayi, ranar dai kwana yayi yana watsawa jikinsa ruwa ko zai rage jin abinda yake ji,gbdy yayi week, jikinsa yasoma sakewa, numfashinsa yasoma barazanar d'aukewa dole tasa ya sake mikewa yayiwa kansa allurar kwantar da sha'awa sannan ya d'an ji dama ajikinsa har bacci yayi nasarar d'aukesa .

****

yau tsawon kwanaki uku kenan ala'meen bai sanya muwaddat acikin kwayar idanunsa ba tunda safe kafin ya tafi aiki ,zai so ganinta amman hakan bata samuwa , idan kuma ya dawo shima baya ganinta saboda wasu lokutan da yamma tana kitchen ,ko a parlour sun daina haduwa ,lokacin da yake zuwa parlour ita kuma tana d'akinta makale da wuyar bunayya, dan haka ko yana son ganinta babu dama ,to idan kuma ya aika kiranta yace daita me ?
shi Gabadaya ma yanayinta firgitashi yake da zarar ya ganta yanxu ne gabansa zai kama faduwa ,sai daya kwashe kwanaki wajen biyar bai sanyata acikin kwayar idanunshi ba, yanzu daya sauko cikin shirin zuwa office yake tambayar eiman "wai me yasa yayarku yanxu bata zaman parlour'n, ko bacci take da wuri?

"Babu wani bacci, kawai dai tana gama cin abinci sai ta shige daki kamar mai yin bacci ,nan kuwa hirarsu suke ita da yaya Auwal a waya ..
Ya d'an zaro idanu kad'an cikin kad'uwa,acikin zuciyarsa yace hirar suke da Auwal ?
"Kwarai kuwa yaya ala'meen, ai sau tare idan kaji tana waya to dashi ne wani lokacin har da dariya zakaji tana yi ,wannan zantuttukan nata yasa ya fahimci ba a zuciyarsa yayi maganar ba azahiri yayita "ai sai ma ka ga yadda suke ji da junansu,, cikinsu duk Wanda bai ji muryar Dan .....
A matukar fusace ya buga mata tsawa "dan Allah malam ban tambayeki duk wad'an nan bazanye surutan ba ,tambaya daya na miki sai wani zuba kikeyi kmr ruwa ,ke kam mijinki nada aiki yana gama fad'ar haka ya juya afusace..

Tabi bayansa da kallo tana ta'be baki "maseefaffen kawai ,ince Kaine ka tambayeni ,ni kuma yazama lazin na fayyace maka komai, idan ma surutu ne ubanwa ya koya min ?
Dubeshi sukai sukai da wuya kamar lagwani ..
ta karasa maganar tana kwashewa da mugun dariya ..

"Yayan kike zagi ,da yiwa dariya haka ?
Taji muryar ihsan daga bayanta "tayi murmushin "ke munafukarsa to ni ba zaginsa nayi ba ...

"To me kikayi idan ba zaginsa kikayi ba?
"Nafa ji duk abinda kika fad'a Dubaishi sukai sukai da wuyansa kamar.. ai da sauri eiman ta matso gaban ihsan ta rufe mata baki "haba yar'uwa so kike yaji ya markad'a min duka ?

ihsan ta cire hannuta a saman bakinta "ai wallahi gara ya lallasaki saboda baki da kunya "to kiyi hakuri yar gaban goshin d'anta na daina ...

A ranar bayan sallar magariba hisham ya ziyarci ala'meen suna samansa suna tautaunawa hisham yace "ni kuwa ina bakuwar gidanku muwaddat madam fa ta dameni da maganarta ..

Al'amen yayi murmushin takaici yana yatsina fuska "ai nima da muke gida daya ba ganinta nake yi ba ...

"Malam cewa zakayi baka so ganinta ba ."wallahi idan dai har zaka yarda yau kwanana biyar kenan ban sata a idona ba ,nima hakan na damu daita Wanda bansan dalili ba gabadaya tunaninta yaki barin zuciyata ta huta ..

Hisham ya buga masa harara "banason maganar banza so dai kawai kake kace min ka fara sonta cikin murmushi ala'meen yace" kusan haka ne ni ban ta'ba tunanin wata yarinya a zuciyata ba sai wannan karon daren jiya fa har kasa bacci nayi amman duk da haka bakaji yadda nake jin tsoron shiga harkarta ba domin na gane take takenta tana da wulakanci..
hisham ya numfasa had'e da cewa
"Abokina ka cire zance wulakanci ai ko tana yi nasan bazata iya yi maka ba ,abinda nake so dai kai, in dai da gaske kana sonta,to kabita a sannu ku saba daga nan sai ka fara nuna mata soyayya, ka tabbata kafin ta koma garinsu ka dasa soyayyarka a cikin zuciyarta ,ala'meen ya sauke naunayen ajiyar zuciya tare da cewa "shikenan sai dai akwai wata matsala fa "
"Ta me kenan ?
"Akwai yaron gidan da'ake rokonta a can,in takaice maka shakuwar dake tsakaninsu tayi yawa , ni sai nake ganin kamar soyayya suke ,duba da yadda zasu d'auki tsawon lokaci a waya suna hira ,kuma idan kaga dariyata ko maganarta da shine, wannan abun na matukar d'aga min hankali fiyye da tunaninka "

"Zancenka zai iya kasancewa gaskiya zai kuma kasamcewa hasashe ne kawai saboda shakuwa babu abinda baya sawa ,sai dai ai last time danazo ai na gansa, ko bawani yaro fari dogo mara kiba mai doguwar fuska da saje mai shegen miskilanci ba ?
"Shine d'an iskan yaro da bai ganin kowa da mutunci in takaice maka har ya gama kwanakinsa a gidan nan kallo arziki ban ishesa ba balle gaisuwa yaro k'arami ya d'auki girman kan tsiya ya d'aurawa kansa, kodan yaga ubansa wani ne oho ?

"Hakan ma zai iya zama sila amman ni yanzu abinda nake so da kai tunda abun yazo hk, ka

samu goggonka ka tuntu'beta, kafin kasoma bayyanawa ita yarinyar soyayyarka, idan akwai wani abu a tsakaninsu sai ka janye ,karka soma bayyana mata soyayyarka ace an rigaka kaga kai babu yadda zakayi tunda wata kusan tafi wata "ala'meen yace 'shikenan zan yi haka amman ni sai naga yaron kmr zai wa muwaddat kad'an a batu na soyayya, sai dai idan saurin ido zai yi..

"Kai dai ba wannan bace damuwarka domin kasan namiji baya kad'an a soyayya ko aure idan tana son shi sai kaga anyi musu aure, an jisu shiru ,kafin wani lokaci ya tirka mata ciki. ala'meen yayi saurin runtse idanunsa saboda d'acin kalmar yana daga masa hannu "ya isheka malam ka daina hasasho wannan rayuwar tsakaninsu, kwakwaluwarka ta hasko maka ni ne zan aureta har ma na dirka mata ciki hisham yasa dariya yana nunasa "wallahi ala'meen baka da mutunci yanzu dai kiri kiri ka'ajeye latifa a gefe "ai kama sheida ne ban ta'ba sonta ba kawai darajar Goggo hajara ne , bazan iya cewa mahaifiyarta banasonta ba ,saboda amintakan dake tsakaninsu amman ni Sam Sam ban ta'ba jin ina son latifa araina ba, "shikena yanzu yaya kenan za'a yi, ni gashi madam tace na karbar mata number muwaddat..

Cikin rawar jiki ala'meen yace bari na kiraka maka faiza sai ta sada ka da ita ,ya fiddo wayarsa ya kirata tana d'auka yace" ki turo min muwaddat da ihsan yanzu ina son ganinsu ...

Hisham ya dubeshi "ni da ka hado da eiman na sha dariya ,tare da cewa abokina ni fa ina son ihsan gara kasani ,tun yanzu ina riko tunda kayi min kwacen babbar to zan koma Kan karamar ..cikin Dariya ala'meen yace "kai tafi can babban banza yar kawar tawa danake ji daita zan d'auka na baka alhalin kafin aureta yazo , zakama mata tsufa, Dan bana jin nan da shekara Goma za'a aurar da ihsan saboda akidar son boko da dady yake da ,idan kaji yadda dady yake zuzuta sai sunyi boko sosai sai kayi mamaki ..

"Okay a she dai zaku aurar daita din komai dadewar ,ai na d'auka sai dai ku dinga jikata kuna sha ,sukayi dariya a daidai lokacin da ihsan ta shigo parlour'n had'e da sallama tana gama shigowa eiman ma ta kunno kai da sallama ta d'an kalli hisham tana fara'a ,tace "eye yaya hisham dinmu lallai kana jin dadi har wata kiba da kasuba ka fara ajiyewa, abun yabasu dariya gabadaya al'ameen ya had'e rai yana duban ihsan "ke wace kizo min da wannan shirmamma.. "wallahi yaya bansan ta biyoni ba kawai nima yanzu na ganta "

eiman tace "a'a karkaga laifinta yayanmu batasani ba ,na biyota dan kar ayi ban dani Dan tunda naji ka kira aunty faiza nasan tasamu ne ,sannan ta juya ta kalli hisham had'e da shagwa'be fuska tace yaya hisham "wai tambayar danayi maka akwai shirme aciki ?

"Rabu dashi mun fi kusa ni dake kinsa bata baci atsakaninmu, yanzu manta da wannan yayan naki yaushe zan zo in kai ki kiyiwa minal yini ?

Tun kafin ta sake cewa wani abu al'amen ya Mike ya korata waje da gudu ta arta tana dariya har da rike ciki ya kalli ihsan yana huci ",ina muwaddat ?
"Tana d'akinta yayi shiru na wasu sakwani sannan yace me takeyi ?

"Gaskiya ban dai sani ba amman bari na duba, ta juya ta fita da sauri ta sauka kasa d'akin muwaddat ta nufa bata sameta aciki ba sai kawai ta nufi parlour'n dady tana ganinta tace "aunty muwaddat wai inji yaya ala'meen kizo ku gaisa da yaya hisham muwaddat ta d'an bata rai "Anya kuwa ni yace miki "kwarai kuwa ke yake nufi muwaddat tayi shiru kmr bazataje ba sai hjy hajara ta galla mata harara ba shiri ta Mike, ita ba gaisawa da hisham bane bata so kawai d'akin ala'meen din ne bata son shiga d'an tunda tazo bata ta'ba yin hanyar bangarensa ba ,amman yau dayake babu yadda ta iya da ranta haka nan ta nufi hanyar tana yin sallama ta yaye labulen parlour'n tashiga..zazzakar muryarta ta doki kunnen ala'meen yadda muryarta ta ratsa jikinsa ko daga bacci ya tashi muryar bazata bace masa ba ,gabadaya suka had'a baki suka amsa sallamar datayi kafin ta gama shigowa kamshin turarenta duk yagama shige musu hanci gabadaya hatta parlour'n ma ya gauraya da kamshinta ,ala'meen dake kishinged'e ya d'an lumahe idanunsa ahankali kana ya bud'esu akanta suka d'an kalli juna kafin daga baya ta kawar da fuskarta hisham na nuna mata gurin zama ta gaishesa sannan ta zauna cikin fara'a kad'an bazakace itace take zagewa da Auwal su raba dare suna zuba surutu ba ,da kyar ta sake bud'e bakinta tacewa hisham" ya gida da madam ?

"madam tana nan lafiya tace a gaisheku suka d'an yi shiru batare da sake cewa komai ba kusan second biyu hisham yace "malama muwaddat me yasa kika da wuyar gani gashi baki son mutane ?
Yanzu da ba Dan na tura a kiraki ba har na tafi bazamu gaisa ba kenan? Murmushin gefen baki tayi "kaga kuma ganina ba wahala garesa ba amman ga Wanda bai kama kansa ba zai wuya ya gani sannan batun rashin son mutane, ni mutane masu shegen surutu ne banaso..

"Al'amen ya jefa mata wani irin kallon da shi kansa bai San yayi hakan ba ,nan Dana ta tamke fuska tana sake kawar da kanta gefe hisham ya cigaba.
hisham yace "shikenan na fahimceki "minal tace ki d'aure ki sake kawo mata ziyara acikin zuciyarta tace "ita idan ta matsu tana son ganina why not tazo ,amman a zahirance cewa tayi InshaAllahu zanje "Kamar yaushe kike ganin zakije ?

Ta yatsina fuska had'e da cewa" babu rana gaskiya amman ina da niyyar zuwa ,sai lokacin ala'meen yayi karfin halin cewa karka yarda da zanceta makaryaciya ce da sauri ta kallesa cike da matsanancin mamakin tare da tsaresa da fararen idanunta "yaushe wannan ya fara atsakaninsu da har zaice mata makaryaciya? kalmar datafi tsana kenan a rayuwarta sai gashi a karon banza a kirata dashi, hisham yayi saurin cewar karyar me tayi maka ?

"Ranar da mukaje gidanka muna dawowa gida sai naji tana bada labarin karya wai taga gidan sarkin garin nan taga gidan gwana kai har gidan zoo tace munje ....
sukayi Dariya hisham yace "ina laifi data kareka.
 "ta dai kare kanta dai nasan tayi haka ne Dan kar gaba a sake tursasata fita..

Muwaddat ta d'an Mike tsaye saboda shirmensu ya fara cika mata kunne dole daman tasan hisham zai kasance kmr ala'meen gurin zuba tmkr ruwa ,tunda sai hali yazo daya abota kan zo daya ..hishsm yace "ya kuma kika tashi ana hira ?

"Ni zan koma ciki idan kaje ka mika min gaisuwata gurin madam"

Ala'meen ya fahimci shi take son ta gujewa saboda kallon dayake mata hisham yace "amm madam fa tabani sako a amsar mata number wayarki a she Ranan nan har kuka rabu baku amshi number juna ba muwaddat tace "mantawa muka yi saboda hira ta d'auke mana hankali anan take ta gaya masa number ya shigar dashi cikin wayarsa yace "baki gaya min sauran lambobinki ba dan naji ance layuka uku gareki cikin yatsina fuska tace "ka manta da sauran tunda za'a iya samuna Akan wannan layin ,hisham yace "haba muwaddat ina ganin ko mutun yana rowar number baya yiwa kawarsa ba ,duk yadda yayi muwaddat ta tsare gida ta hanna sauran number's dinta Wanda tabashi din ma ta karamar wayarta ce datake amsa kira Wanda abi ya tsiya mata ,wai saboda koda cajin babbar wayar ya kare, Dan bayason yakirata bai sameta ba ..

shi kuwa hisham Dan dai yajata da hira sai cewa yayi "ke din da nake son ki zama surukata sai gashi kun kulla kawance da daman ..

Da sauri tace wace irin suruka kuma ?
"Au baki da labarin ina rikon ihsan ko?
Cikin dariya tace "da dai faiza kace me yuwa na Dan tsaya maka tunda ita ihsan ai uban gidanta na hannun damanka ne ..

Hisham ya jiyo ga ala'meen dayazamanto tamkar sauna a zaune yana kallonta ",kai maigidana kaji abinda surukata ta fad'a....

Ala'meen yayi murmushi yace ",ai ina ganin ko ita surukar taka a halin yanzu bata isa aure ba bare aje ga faiza ko ihsan, hisham yace "haba babban yaya karka raina min hankali mana kawai saboda ba'ason bani kanwa sai kuma ace yaya ma bata isa aure ba ,kina jinsa dai big sister ya fad'a tare da kallon muwaddat.

Ta d'an kawar da fuskarta gefe "eh to abinda ya fad'a gaskiya ne, sai kaje kayita jiran lokacin idan kaji zaka iya "kenan idan na fahimci ki kenan kin goya masa baya akan maganar sa na cewa kema baki isa aure ba ballanata kanwarki?

Ta sake had'e rai "wannan ai maganarku ce ni dai na tafi ka gaida gida tana shirin fita daga parlour'n sai ga eiman ta biyota da wayoyinta big sister an damemu da kiran wayarki muna cikin kallo an hanamu jin gari ya Auwal yakira wasu ma duk sun kira ni dai nace musu kina d'akin yaya .....

Cikin matsanancin jin haushi muwaddat tace ",to d'an me zaki biyoni da waya d'akin mutane ,ko ance miki dadewa zanyi ,Muje gani nan saukowa eiman na shirin fita aka sake bugowa ta juyo da sauri "to ga Auwal nan ya sake kiranki .

Cikin tsawa tace dan rashin da'a kai tsaye kike kiran sunansa bako rusunawa ?
Bata amshi wayar daga hannunta ba har kiran ya sake katsewa "oya maza ki koma da wayar idan na sauko zan kirasa ..

"Ni gaskiya ki amshi wayar a hannu , ni yanzu meye laifina bayan agabansa bazan kira sunansa kai tsaye ba "ki ma yi kiga yadda zai yi kaca kaca da namanki Dan kinsan shi baya d'aukar shirme ..

eiman ta marairace" murya big sister Dan girman Allah ki taimaki rayuwata ki amsa kinga na rigada na d'auka da farko ,kinsan Halinsa zai d'auka ban kawo miki bane ...

Gabad'aya daga muwaddat din har eiman a tsorace suke ita eiman najin tsoron kar idan yazo yaci ubanta, Dan bai mantuwa, sannan bai yafiya duk dadewar Abu zai hukuntaka akansa, sai dai idan yagadamar Kyaleka, ita kuma muwaddat rashin sanin abinda zata fad'a masa idan ta ashi wayar take, cikin haka ya sake kira "kin gani ko big sister ya sake Kira Dan girman Allah ki rabani da wayar nan .

Ala'meen kasa d'aurewa yayi yace "shi din waye da baza iya amsa wayarsa anan ba ?

"Batare data juyo ba cikin tausashiyar murya kmr zatayi kuka tace "auwal kanina ne fa, sannan ta amshi wayaoyinta ta bar d'akin cikin 'bacin rai , itama eiman sai lokacin ta saki ranta ,tana sakawar a'lameen murnushin Wanda za'a iya kiransa,Dana mugunta ...

ji ,dan haka shi ke satar hanya ya bi ta kofar kitchen ya kirata tazo ta bud'e masa kofar yashigo su nufi d'akinta ..

****

Wasa wasa shakuwa mai tsananin karfi ta sake tashiga tsakanin Muhammad Auwal da muwaddat ,a bangaren bunayya yana jin dadin akan yadda take bashi hadin kai ,yanzu har agaban su ummi soyayyarsu suke barjewa batare da sun hankalta ba ,duk yadda ummi ta kai da sa ido akansu, da duk wani motsinsu haka ta gaji ta hakura saboda ta kasa fahimtar komai ,hatta dan had'a jikin da bunayya ke son yi da muwaddat ada ,yanzu babu ya daina baya kwata kwata baya shiga harkarta..

A yau ne aka wayi gari ummi zata tafi bikin diyar aminiyarta da za'ayi kamar yadda tayi niyya, sam bata so tafiyar tabar muwaddat ba, amman babu yadda zatayi ,kirkin hajiya saratu daban ne acikin mutane, tana da matukar kirki da kima a idanunta shiyasa ta kudirci aniyar haltar bikin .

jirgin yamma ummi zatabi zuwa minna ,muwaddat da bunayya ne 'yan rakiya ,yana zaune gidan gaba gefen direba ummi da muwaddat na gida baya ,muwaddat sai wani shagwa'ba take wa ummi" wai zatayi kewarta "kiyi hakuri bby naso zuwa dake wallahi kodan kije kiga binki nufawa 'amman karki damu idan zan koma binki sadear InshaAllahu tare zamu ,bayan jirgin ummi ya tashi suka dawo gida bunayya sai faman murna yake zai ci karensa babu babbaka .

Gidan zai saura daga su sai binta mai aiki gashi ita binta Sam bata da saka ido irin na baba mai gadi, itama dai ji yayi da yana da inda zai aikata daya turata Kafin ummi ta dawo domin yasamu damar watayawa ,amman dai duk da haka zamanta ba zaizo da wata matsala ba, dan bazai hanasa abinda yake so ba, tunda masoyiyarsa zata bashi had'in kai a duk sanda yaso ....

Ummi na barin gidan ko cikakken awa biyu ba'ayi ba bunayya ya nufi d'akin muwaddat ..

Mmn sudais ce
2/4/20, 8:39 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

alhamdullahi am back again.

warning!!!

for the first time !!!! i will like to say," don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....wannan shine.

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

page 32

....tana komawa d'akinta, ta fad'a saman lafiyayen gadonta ta kwanta lamo tana jin yadda jikinta yake k'ara moving akan matsanancin soyayyar bunayya ..

ta rasa dalilin da yasa take jin haka a sansar jikinta a duk sanda ta kasance tare dashi ,da kuma sanda take ita kad'ai, sai tayita jin jikinta yana mata wani iri ko Kuma ta dinga jin salon wasaninsa a sansar jikinta suna yawo a kowani shashi na gangar jikinta mai kama da socking .

Ahankali soyayyarsa da romacing dinsa ke yawo a jinin jikinta , ta runtse idanunta saboda a halin da take ciki yanzu tana bukatar hutu ba dogon tunanin ba ,dan ta murzu a hannunsa sosai fiyye da tunanin mai karatu ..

har kusan la'asar tana kwance akan gadonta , ba tasan lokacin da binta mai aiki ta dawo gidan ba ,bugun kofar d'akinta da'ake yi ne yasa ta bud'e idanunta da kyar saboda har lokacin bacci na cikin idanunta, ko bata tambaya ba, tasan ciki biyu za'a yi d'aya ko binta mai aiki ce ko kuma bunayya, ahankali ta sauko daga kan gadon tazo bakin kofar ta bud'e , binta mai aiki ta

gani tsaye tana dubanta "ya'akayi mama binta da yake haka take kiranta ?

binta mai aiki tace" babu komai 'yar d'aki , na dai ji shiru shiru baki fito tun sanda na dawo, gashi har lokacin sallah la'asar ta qaratowa, baki tashi ba, lafiya dai kike ko ?

Muwaddat ta d'an yatsina fuska sannan tace" lafiya nan dai da sauki mama binta wallahi zazzabi nake ji "

"a sha Allah ya sauwake daman nasan za'a rina tun kafin na fita fa kike nuku nuku a d'aki har yanzu ,to ko za'a kira auwal yayi miki allura ne kafin ya fita ,dan gashi can kamar fita zai yi?

"no ki barshi kawai zan sha magani, ciwon kai ne kawai ke damuna "to shikenan bari na koma bakin aikina, amman dai karki koma kwanciyar nan ta isa haka .

muwaddat tace "to had'e da juyawa ta koma cikin d'akin tana mai rufo kofar batare da tasanya mata key ba, binta mai aiki ta juya, kai tsaye bayi ta shiga ta sakarwa kanta ruwa tazo tayi sallah .

tayi wanka ya kai sau uku , amman har lokacin jikinta zafi gau tamkar garwashin wuta sai daga baya jikinta ya d'an yi sanyi ,sai kuma bacci barawo ya d'auketa .
Wunin ranar akwance tayisa sallah ne kawai ke tada ita , gabad'aya ta rasa abinda ke mata dadi arayuwarta ,ta kasa sakawa cikin komai , wani irin miyo ne ya tokare mata makoshi wanda ya addabi rayuwarta , duk yadda taso ta had'iye abun ya garara, dole tashiga tarawa acikin bakinta jifa jifa ta Kan tashi ta shiga bayi ta zubar ta sake dawowa ta kwanta akan gadonta, har dare tana kwance a d'akin batare da tayi yunkurin fitowa ba, hatta abinci dare nan binta mai aiki ta biyota dashi ,da kyar binta ta tursasata tashi tasoma d'an tsakurar abincin , sai dai tana gama ci sai yunkurin amai, nan fa hankalin binta yayi matukar tashi ,a gigice tayi hanyar bayi daita , muwaddat ta durkusa rike da cikinta da goshinta tana kwara amai ,yayinda binta ke tsaye akanta tana jera mata sannu .. har sai data amayar da duk wani abinda ke cikinta, tana cigaba da yi mata sannu ,"sannu yar d'aki ...."
tare da Mika mata ruwa ta wanke bakinta da fuskarta, sannan ta taimakamata suka dawo d'akin ,ta jingina bayanta da pillow kana tace " yar d'aki baki da lafiya ,jikinki yayi zafi dayawa amman kin hana a fad'owa bunayya ya taimaka miki.
Kai kawai iya ta girgizawa binta ta janyo numfashi da kyar ta fitar tace "ai naji sauki mama binta ,yanzu babu abinda ke damuna , ta fad'i hakan kawai dan binta ta fita daga d'akin ta samu ta kwanta dan har lokacin juya take gani,shiru ne ya ratsa d'akin binta mai aiki bata sake cewa komai ba,kamar yadda muwaddat bata sake cewa komai ba , batare da 'bata lokaci ba binta ta tattara kanukan abinci tayi hanyar waje ,tana yi mata sai da safe ....
Bayan fitar binta ta zame ta kwanta tana fidda numfashi sama sama tmkr mai cutar asma ahankali har bacci ya d'auke ta.

cikin dare taji mutsumutsun mutun ajikinta yana lalubarta tare da lasar gefen wuyanta zuwa

dukiyar fulaninta ,lokaci d'aya ta bud'e idanunta tana k'ok'arin kunna wutar d'akin , yayi saurin riko hannuta yace "me zakiyi ?
" ki yi baccinki kawai babu abinda zan yi miki kawai tumin jikinki zanji yayi mganr yana buso mata numfashinsa da iskar bakinsa.

muwaddat ta d'an lumshe idanunta tana jin yadda numfashinta dana bunayya ke gauraya guri d'aya , cikin murya mai cike da kasala yasoma magana "a she karya kika min ko?
"karya me nayi kuma tayi mgnr a shagwabe ?
"kika ce ummi zata dawo yau ashe sai gobe ..
"uhm nayi haka ne saboda na rabu da nacinka.."

"aiko karyarki ta sha karya yarinya ,dan wallahu ba zaki ta'ba rabuwa da nacina ba ,har duniya ta nad'e, saboda kin zama ni ,na zama ke ,gashi bana gajiya dake, a duk sanda na kalleki soyayarki na sake tsuma zuciyata ,dama gangar jikina ....
"na sha gaya miki kece rayuwata ,kece duniyata amman na lura baki d'auki hakan da mahimmancin ba shi yasa Kika ki fito da soyayyarmu fili bare umminki ta fahimta ta amince da aurenmu ....

Cike da wani irin salo mai wuyar misaltuwa ta shige jikinsa sosai tana mika ,wanda hkn da tayi ya janyo jijiyarsa tayi saurin harbawa ..ya lumshe tsumammun idanunsa yana shafa sumar kanta daya samu nasarar zubowa gadon bayanta ..
Muryarta cike da zolaya tace " ai koda su ummi sun amince da aurenmu,ni bazan aureka ba, domin na tabbatarwa kaina kafi karfina a halin yanzu , dan bazan iya da kai ba...
"kullun abun d'aya ba'a gajiya kamar wani inji, yaro da kai sai jaraba tsiya"
ya kai bakinsa ya ciza gefen kunnenta yace "ya ne za'a yi haka Allah ya haliceni, ai ke ma irina ce shiyasa muke mugun son juna .....
Ko na rabu dake ina da tabbacin bazaki barni ,bare Kuma ni dake mutu ka raba ya k'arasa mgnr yana manna mata hot kiss ....
Take tasoma d'auke wuta ganin yana neman canza salo tayi saurin taka masa burki dan haka ya cigaba romancing dinta sama yana fad'a mata kalaman soyayya masu sanyi da dadi batare da sunyi komai ba ,ya ta'ba nan ,ya tsotse can ,haka dai har bacci yayi nasarar d'aukarsu suna makale da juna ....

can tsakar dare jikinta ya sake d'aukar zafi rau , zafin jikinta ne ya tayar dashi daga baccin da yake, ya tashi zaune ya tsura mata ido yana kallonta , jin al'amun baya tare daita yasa ta bud'e idanunta ahankali tana nishi sama sama , ya kamo hannuta ta mike zaune , suna fuskantar juna, ya kai hannunsa ya shafa fuskarta yace "daman baki da lafiya ne naji jikinki yayi mugun zafi haka ?

ta yatsina fuska kmr zatayi kuka tace "dazu ne fa naji gefen kaina na min ciwo, amman ai naji sauki, yanzu ne kuma
zafin jikin ya dawo "to me yasa baki kira kin fad'a min ba?

Muryarta a raunane tace "gani nayi naji sauki "
yayi shiru kawai yana cigaba da kallonta ahankali cike da shagwa'ba ta fad'a jikinsa ,da sanyi jiki ya soma tattara gashin kanta Yana k'ok'arin tufkesu guri d'aya ,d'akin ya d'auki shiru yadda bai sake yunkurin cewa komai ba ,haka zalika itama bata sake cewa komai ba, har sanda ya gama had'e gashinta, tana kwance lamo ajikinsa yana tunanin yadda yake ganin yanayinta acikin kwanakin ,har ga Allah baya karfafawa zuciyarsa abinda yake zarge a tattare daita ,ba dan komai ba ,sai dan saboda tabbacin daya samu daga gareta akan al'adarta .
Ahankali ya kawar da zance zucin da yake ya kamota ya had'e fuskokinsu ya kamo lips din yashiga tsotsa yana sake janyota jikinsa ya rungumeta tsam ,yana shafa bayanta zafin jikinta na ratsashi ,cikin mayunwanci hali ta cire bakinta daga cikin bakinsa tana sauke naunayen ajiyar zuciya .
Shima ajiyar zuciya ya sauke yace "bari naje na kawo miki magani har allura ma sai nayi miki ko?

ya yunkura zai sauko daga saman gadon tace "ka barshi kawai bari na watsawa jikina ruwa zafin zai lafa ya marairaice mata kmr zai zubar mata da hawaye "haba kar ki min haka Mana .." ki bari na kawo miki magani ki Sha ki samu sauki .
tace "ba wani abu yasa kaji na fad'i hk ba, saboda idanun mutane ne, kasan ba mu kad'ai bane acikin gidan nan ba, akwai abi sannan binta mai aiki na nan, itama, karkaje tsautsayi yasa kayi kicibis da daya daga cikinsu,aga ka fito daga d'akina a daidai wannan lokacin me zaka fad'a musu?

yayi shiru kawai yayi yana kallonta saboda, yasan ta fishi gaskiya, dan haka da kansa yayi mata wanka suka dawo kan bed, ya sanyata cikin jikinsa, duk da haka dai batayi ishashen bacci kirki ba saboda tsananin zazzabi.

babu laifi washegari ta tashi zazzabin da sauki, tana kwance a d'akinta ya kira wayarta tana d'auka ya tambayi jikinta, sannan ya k'ara da cewar tazo bangarensa ta amshi magani tace "taji sauki ya bar maganinsa,yace "sosai kika ji sauki babu inda ke miki ciwo ?
tace "eh "

"to ki dai zo part dina yanzu ina son naji dumin jikinki da kaina ,dan na tabbatar da lafiyarki, tayi shiru taki cewa komai, yace "kin yi shiru kina jina ko ba zaki zo ba, ni nazo da kaina na sameki? da sauri tace" no karka zo plz wallahi har yanzu abi na gida bai fita ba, bai sake cewa daita komai ba ya mike ya nufi bangaren ummi a daidai bakin kofar suka had'u da abi ya rusuna ya gaishe dashi ,abi ya amsa cikin sakin fuska tare da cewa kana nan dai kana shirin tafiyarka ko? ya kai hannunsa ya shafa sumar kansa yace "ina kan yi , sati na sama nake sa rai zan wuce Inshaallahu "to Allah ya taimaka, Allah ya nuna mana lokaci, idan kana bukatar wani abu kasanar min "okay abi Inshaallahu i will, abi ya sa kai ya fice shi kuma ya shiga parlour'n yana shiga ta fito daga cikin d'akinta cikin riga da siket ta yafa mayafi daya bi da kalar kayanta tana ganinsa ta had'e fuskarta taki bari annuri ya bayyana akan fuskata sbd ta tabbatar matsawar ya k'araso gareta ,sai zance ya Sha bambam , wani abun zai mata, dinning area ta nufa kai tsaye

ta ja kujera baya ta zauna ta meida kanta kan abinci shima ya ja kujera ya zauna bai ce mata komai illa hannusa daya kai gefen wuyanta, babu laifi normal jikinta babu zafi.

 ta cire hannunsa ta d'auki plet biyu zata zuba masu abinci yace "ki had'a mana muci tare mana ,taki kula shi ta zuba abinci daban daban ta tura plet gabansa tasoma cin nata tana kallonsa ya janye abinci data tura gabansa gefe yasoma ci cikin nata suna cikin cin abinci ya amshi spoon dinta ya ajiye ganin ba wani abinci kirki take ci ba yasoma bata da farko kin amsa tayi sai dataga yana shirin 'bata mata lokaci sannan ta bud'e bakinta tasoma amsa.

ya dibi abinci ya kai bakinta kenan ,ita Kuma ta bud'e bakinta da niyyar amsa ,sukaji ana k'ok'arin shigowa parlour'n ,take gaban muwaddat ya fad'i ya shiga dokawa da sauri , ta rud'e ta gigice tama rasa me yakamata tayi guduwa zata ko kuma zama zatayi ta cigaba da amsar abinci,kafin kace me jikinta ya d'auki rawa saboda bata son abi ummi ko binta mai aiki su ganta tare dashi a wannan halin,cikin rawar tasoma k'ok'arin mikewa da niyyar guduwa bunayya ya riko laulausar tafin hannuta yana kai abincin bakinta"ka bari mana ba kasani ba ko ummi ce.....
ko gama rufe bakinta ba tayi ba abi ya bayyana cikin parlour'n aiko jikinta ya sake d'aukar rawa tayi saurin sunkuyar da kanta kasa kirjinta na bugawa da karfi , shi kuwa bunayya waskewa yayi ya sakar mata hannu ya kai spoon din abinci bakinsa, sai bayan da abi ya gama kallonsu tsab sannan yace "kin gama Shirin zuwa makaranta dan yanzu umminki ta kirani wai mu saukeki a ?

da sauri ta d'aga masa kanta sama, al'amun eh, bunayya dake cin abinci yace "abi kayi tafiyarka kawai zan sauketa "a'a umminku tace ni da kaina na.. .....
Yayi saurin katse abi ta hanyar cewa "to ni cinyeta zanyi ne , da ummi batason na kaita ?

"wannan kuma tsakaninku ne babu ruwana ,yayi mgnr yana murmushi sannan ya nufi hanyar d'akinsa bunayya ya tsura mata ido "matsoraciya kawai ke komai tsoro yake baki?
"Kalli duk yadda Kika wani rude, Kika gigitace.
ta yatsina fuska kmr zatayi kuka tana kallonsa ido cikin ido domin alokacin sam bata so abi ya gansu a yanayin daya taddasu ba ..

murmushi yayi "to ai sai ki sanyawa jikinki natsuwa tunda yashige, the next thing km ki maida hankali mu k'arasa cin abincinmu ,tsaki taja tare da kai masa duka a saman kafad'arsa, murmushi kawai yayi yana shafo tsakiyar tafin kafafunta da nashi yatsun, wani irin zirrrrrr taji tayi saurin lumshe ido "wai kai bunayya me yasa kake yin irin hk ne...?
 "me nayi kuma yayi mgnr yana son daga murya tayi saurin rufe masa baki tana bashi hakuri,"yi hakuri bance ka tara min mutane ba "
Ki taimaki kanki dan ni babu ruwana da duk wani mai ganinku idan ba'a son ganinmu hk ayi mana aure .."haka kawai mutun da rashin da lafiya yace Yana son aure a tauye Masa haki ,wallahi tallahi kema zaki jawowa kanki ,dan abinda baki so shi zan dinga yi miki .ta kwa'be baki

"meye shi ?
Ya ware kafafunsa yace "ci ta hanci ta baki takoina da wahalata ta isheki zaki San yadda zakiyi Dani "kai ni rabani da riginarka ..

cikin minti kad'an suka kammala cin abinci har lokacin abi bai fito ba ya tsura mata ido yana kallonta gashi dai tashi take son yi tun kafin abi ya dawo ya samesu hk amman ta kasa ,cikin zalaya tace "kaga malam dan Allah ka daina min irin wannan kallon, ta'be bakiyi yayi "ke da wani ido kikaga ina kallonki?
yana gama fad'ar hk ya Mike tsam ,cikin zolaya yana k'ok'arin bar part din ummi..yace " aunty ki shiryawa anjija da wuri nima zan dawo zabani na rana naci kafin umminki ta dawo ta kanainaye koina .....
Banza tayi Masa taking cewa komai har sansa ya k'arasa barin parlour'n.

muwaddat na shiga makaranta tasoma jin zazzabi sakamakon wani turaren abokiyar karantunta data shaka,gefen kanta ya sara abu kmr wasa sai gashi tana kelaya amai duk abinda tace sai data amayar dashi acikin kankani lokaci ,ta fita haiyacinta har wata yar daguwar rama tayi, tayita d'aurewa ,da taga abun na son fin karfinta ta kira number abi tace a turo mata direba bata da lafita, madadin abi ya tura mata direba kmr yadda ta buqata sai ya tura Mata bunayya, inda yake fad'a ya kula daita ta hanyar taimaka Mata , cikin kankani lokaci ya k'araso ya d'auke zuwa Gida ,tunda ta isa gida tashiga d'akinta da kyar ta kwanta bata sake fitowa ba, Taimakon gaugauwa ya fara bata tare da maganin malaria a tunaninsa itace ke son takura Mata , tunda complain din ciwon kai take , byn ya bata magani ya kwantar daita ajikinsa Yana k'ok'arin rabata da kayan jikinta duk yadda taso ta dakatar dashi ta kasa saboda bata da kuzari ajikinta ahankali ya rabata da kayan jikinta,shima ya cire kayan jikinsa ya had'eta jikinsa yana shashshafata zafin jikinta na ratsa jikinsa , ko cikakken minti goma Basu d'auka a haka jikinta yayi sanyi ,Aiko ya birkice mata ,ta hanyar turo Mata zafafan sakoninsa masu tsayawa arai , tun tana zamewa ajikinsa ya tarairayota har ta bada kai ,suka lula duniyar soyewa , yau kam ba tayi Masa wani raki ko korafin gajiya ba, ita da kanta ma ke sake makaleshi ajikinta,tana shafosa ahankali suka cigaba da murza fatan juna batare da tunanin want ba .....

jirgin yamma ummi ta biyo ,karfe 4:00 daidai na yammaci ranar ta sauka, tana sauka number muwaddat tasoma nema kafin na kowa, sai dai wayar na ringing,amman ba'a d'auka, ta k'arasa inda tasan zata ga direbanta.

bello direbanta na ganinta ya fito da sauri daga cikin motar, yana k'ok'arin bud'e mata kofar baya had'e da gaisheta ta amsa sannan tashiga ya ja.

suna isa gidan babu wanda ta soma tambaya sai muwaddat, binta tayi mata sannu da zuwa sannan ta k'ara da cewa" dazu ta dawo daga makaranta tana d'akinta kai tsaye d'akin ummi ta nufa....

Mmn sudais

2/4/20, 8:39 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

warning!!!

don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....

WATTPAD @HAUESH

Page 33

..Hannu ummi ta kai jikin handle din kofar d'akin domin bud'ewa ,taji kofar a rufe gam ,dan haka tashinga buga kofar da karfin gaske cikin tsananin tashin hankali tana Kiran sunanta" muwaddat! Muwaddat!!

Muwaddat dake kwance a saman fad'ad'den kirjin bunayya tana baccin gajiyar sex din da sukayi , ta zabura tai wani irin hantsilowa daga kan gadon cikin tsananin tashin hankali tana dafe kirjinta da duka hannuwanta tare da furta kalmar" Inna lillahi wa Inna ilaihi raji'un "yau mun shiga uku..ummi ta dawo...."

Wani irin shu'umin kallo bunayya ya bita dashi kana yace "mun shiga uku ,ko kin shiga uku?

Murayarta na rawa tace " duka mun shiga daga ni har kai wallahi ...irin abinda nake gudu kenan amman ....
"wata uwar
Harara ya zabga Mata Wanda yasa take ta had'iye abinda take son furtawa , k'ok'arin d'aukar wondansa yayi ya saka hankalinsa a kwance , ya kai hannunsa ya janyo farar rigarsa dake yashe kasa ya rataya a wuyansa " madam please open the door for me...."
"What ta furta a kid'eme tana girgiza masa kai?
"dan girman Allah karka min haka bunayya, ba..banason ummi ta ganmu tare ....." ka rufa mana asiri bunayya ,ta kamo a hannuwansa cikin rud'ewa da matsanancin tashin hankali ,jikinta na sake d'aukar rawa sakamako sake Kira sunanta da ummi tai "muwaddat zo ki bud'e min kofar ,ko jikin ne yayi tsanani ?
Bata amsa illa jikinta daya kama rawa tmkr mazari "zo ..zo muje ka fita ta window tayi hanyar window d'akin dashi ....

Da sauri ya fixge hannuwansa dake cikin nata yana nuna kirjinsa da yatsan hannunsa " ni ne zan fita ta window ko wa?
tayi saurin d'aga masa kai al'amun "eh"
"Dan Allah ka rufin mana asiri ni da kai ,ban ta'ba sanin haka tashin hankali irin wannan yake ba sai yau ,kwata kwata na manta cewar yau ummi zata dawo ..... ta k'arasa mgn hawaye na gangarowa bisa kuncinta.
"ka rufa min asiri bunayya ,"ka taimaki rayuwata ka rufa min asiri bunayya!!tana mgnr tana kuka tana jujjuya Masa hannuwanta tmkr wata k'aramar yarinya , bakinta na rawa tana k'ok'arin kai gwiwowinta kasa ..
ya kai hannunsa ya kamota jikinsa zai rungumeta, ta yi saurin gocewa tana kuka "to yanzu me kike son nayi ,ni dai gsky bazan iya fita ta window ba Allah ya sani , Koda kuwa hkn bashi da wata illa ,bare Yana da ?

"Yanzu haka kina sake
' bata lokaci ne ,har sai kinsa ummin ta fahimci wani abu, ki bud'e kofar kawai ta ganmu ,ba sai na fad'a Mata cewar Abi ne yace na taimaka na duba lafiyar ki ba.....

"ni..ni..dai a'a ,ummi nada saurin fahimta abu, hanyar bayi ta nufa dashi tana kuka "muje bathroom dan Allah karka a'a .. suna shiga suka tsaya cirko cirko suna duban juna ,shi kam bunayya ko dar bai ji ajikinsa ba ,asalima tsumammun idanunsa ya tsura mata yana k'ok'arin rungumeta a ajikinsa, "muwaddat ki natsu plz duk kin wani rud'e ,ki samo mana mafuta , ummi fa zata iya shigowa nan is better ta ganni a bedroom dinki akan nan ....
ba tace dashi komai ba, illa hawaye data cigaba da zubarwa tana k'ok'arin barin jikinsa kafin kace me jikinta ya sake d'aukar zafi ,hankalinta a matukar tashe ta fito daga cikin bayin tana kulle kofar tare da Murd'a key ta zare , jikin na rawa ta shiga gyara gadon dan gabad'aya ya hargitse a wasaninsu , ta janyo doguwar rigarta ta Sanya , ta nufi kofar d'akinta wanda zuwa lokacin har ummi ta juya da niyyar zagayowa ta dubata ta window ,tana gama bud'e kofar ummi

ta juyo da wani irin sauri ...

Lumshe idanuwanta tai tana saisaita natsuwarra kana ta juya ahankali tana dafe kanta da take jin yana Sara Mata tmkr zai cire tsabar tashin hankali ,fad'awa tai kan gado tana fidda numfashi sama sama ta sake sanyawa jikinka natsuwa .

Ummin ta k'araso da sauri zuwa inda take kwance ,ta tsura mata ido tana kare mata kallo, saboda doguwar ramar data ga tayi, ahankali idanunta ya sauka akan kirjinta gabanta yayi wani irin mugu mugun fadawa kafin daga bisani ya shiga dokawa , kirjinta taga yayi wani irin mahaukacin cikowa , yayi mata hake hake ,numfashinta na sauka ahankali ,girgiza kai tashigayi tana kawar da abinda taji ya tsarga Mata acikin zuciyarta "a taanake tashiga kallon d'akin still zuciyarta na dokawa Wanda ta rasa abinda yasa hk hk Nan take jin tsinkewar zuciyar ...

Jikinta a sanyaye ta samu guri a gefen katifa ta zauna ta d'aga kan muwaddat ta meida kan cinyarta, taji zafin da jikinta yayi ,ya ratsata ,ta dafa goshinta tana kiran sunanta ahankali "muwaddat dina..... ...Sannu "
"shi yasa hankali yaki kwamciya a duk wuni yau ,ashe baby nah bata da lafiya"

muwaddat ta bud'e idanunta da kyar tana duban ummi sannan ta kirkiro murmushin dole tana mikewa da kyar ,ummi tace "kiyi kwanciyarki ma ,ina da ina ke miki ciwo?
"ko kanki ke ciwo ta fad'i hakan, saboda tasan tana da yawon ciwon kai, muwaddat dake atsorace ta rasa mai zatace Mata , kawai ta d'aga mata, saboda ita alokacin babu abinda ke damunta sai tsananin tsoron dake tattare daita .

 jikin ummi na rawa tace "okay bari naje na kawo miki magani ki Sha ,wannan zafin jikin naki ya wuce
 kaida, ta ajiye kanta akan pillow ta nufi kofar fita cikin sauri ,kai tsaye ummi hanyar d'akinta ta nufa .

 cikin wani sauri muwaddat ta zabura ta mike, jikinta na rawa ta bud'e kofar bayi ta janyo hannusa ,suka fito tare dashi tana rokonsa ya fita kafin ummin ta dawo amman kememe bunayya yace "bai zuwa koina , aiko ta d'aura duka hannuwanta bisa kanta ta rushe da wani irin kuka mai ta'ba zuciya ....

Naunayen ajiyar zuciya ya sauke da karfin gaske yace "Kinga fa wannan shirmen da kike yi Allah shin zai saka ummi ta fahimci wani abu ,ki natsu ki kwantar da hankali ...ta d'ago da sauri tana kallonsa da idanuwanta da suka gama canza kala tsabar tashin hankali..
  Ummi kuwa nashiga d'akinta ta nufi dorowarta dake ajiye magunguna ta d'auko mganin zazzabi da Maleria ta dawo d'akin muwaddat cikin sauri .. turus tayi tana binsu da wani irin kallo mai cike da tambayoyi iri iri .

Muryarsa a kasalance yace" ummi sannun da zuwa,"yauwa Daman kana cikin gidan ne ko

yanzu ka shigo ?
Bayan keyarsa ya tsutsa Yana duban muwaddat dake k'ok'arin runtse idanuwanta,kana ta rufe fuskarta da hannuwanta yace "yanzu nashigo "

"Okay to d'an bamu guri zanyiwa baby allura ..lumshe idanunsa yayi yana shafa sumar kansa ,sannan ya soma k'ok'arin ficewa daga d'akin,magani ummi ta'bata had'e da yi mata allura still zuciyarta na cikin taskon Dan har lokacin ummi Bata daina jin fad'awar gaba ba, kwantar daita tayi ,tana sake jero Mata sannu ,kusan minti goma ummi na tare da ita kafin daga bisani ta fito ta sake nufar dakinta .

Ummi na fita daga d'akin ta mike zaune tana d'aga hannuwanta duka sama ta shiga yiwa Allah godiya ,daya rufa Mata asiri ,aranta tayi alkwarin babu ita babu bunayya har karshen ratuwarta, ita dashi sai dai kallon kallo bazata sake barin ya kusanci inda take ba ,tunda yafi kaunar ganinta cikin tashin hankali ,kafin wani lokaci zazzabi jikinta ya sauka, ta dawo normal sai dai yanayin jikinta da take jin shi wani iri kmr banata ba komai a sanyaye take yinsa gashi bata jin dadi bakinta komai taci kmr zata amayar ...

****

da daddare yaya al'ameen ya kirata sai da ya soma had'ata da 'yan'uwanta suka gaisa sannan suka shiga hira , wanda duk hirar shine ke yinsa amman ita daga uhm sai uhmm, ba wani abu yake fad'a mata mai Dadi ba ,illa sake jadadda mata yadda tayi tasiri arayuwarsa, jinsa kawai take saboda gabad'aya zantuttusa sun isheta ,koma tace haushi suke bata ,km amatsayin shime ta d'aukesu, tana zaune ummi tashigo parlour'n cikin shiga ta alfarma duk yadda ta d'an manyata hakan baya hanata yiwa mai gidan kwaliyya ,bare anyi kwana biyu ba a had'u ba ta fad'i hakan a zuciyarta , tana gani shigowar ummi ta katse kiran,tana duban ummi .

bayan ummi ta samu guri ta zauna ,ta d'an dubi muwaddat, "ke da waye a waya?
"yaya al'ameen ne ta fad'a mata atakaice, ummi ta kai hannu ta amshi wayar tana dubawa sunansa ta gani sannan tashiga bincikar wayar babu komai na aibu aciki dan haka ta mika mata wayar .

"ya jikinki naki yanzu hope you are feeling better ?
ta d'aga mata kai ahankali ,sannan tashiga janta da hira tana
bata labarin yadda bikin minna ya kasance"baby muwaddat idan kikaga yadda binki fadila ya k'awatu abun sai ya burgeki , sai naji ina ma bikinki ake yi ,amarya da ango sun sha kyau har sun gaji , kema dai zuwa yanzu yakamata musan mai kike ciki da al'ameen, yaron nan na da kirki da hankali matuka ,uwa uba yana da natsuwa sannan ya had'a Master's dinsa zaku dace da juna, dan irin miijn da nake miki fatan samu kenan arayuwarki ,wanda nasan kema shine irin zabinki dogon namji kyawawa mai haiba ko ba hk ba?

muwaddat ta had'e rai sosai tana turo baki, ummi ta cigaba "amman ke sai naga kmr kina basarwa a duk sanda aka yi miki maganarsa,ke kowa yazo kice bai yi miki ba gashi wannan

shekarar zaki kare karatunki, zan so ki saida miji , da zarar kin gama karatunki musha biki "gaskiya ina sonki da al'ameen sosai sai dai bazan matsa miki ba, idan kinji baki sonshi shikenan sai a bashi hakuri shima kmr sauran ...
 muwaddat tayi shiru kawai tana sauraron ummi har tagama maganarta.

ummi ta du'beta sosai tana nazarinta kafin daga baya tace "kinyi shiru shima bazaki auresa ba ko?
 kin fi son kiyita ganina ina yawon zuwa bikin mutane, ni kar azo nawa?
muwaddat ta girgiza mata kai kawai ala'mun a'a amman a cikin xuciyarta cewa tai lokacin da nake son aure ba'a min ba ,sai yanzu za'a dameni to ni banason Yaya al'ameen .....

Kmr ummi tasan abinda ke zuciyarta tace "nifa bazan Miki auren dole ba sai Wanda kike so zan baki ,idan baki son shi abar zancesa kawai ,amman idan kin amince kin yarda da auri al'ameen nasan kowa zai ji dadin wannan had'in.

a kasan zuciyarta kuwa cewa tayi "ni auwal fa nake so ummi bawani Yaya al'ameen ba ...,da zaki aura min shi da kin gama min komai ,da na samun duk wani jin dadi duniya ,"auwal shine cikar burina da kwanciyar hankalina, duk wani wanda zaki so na aura ,bazai ta'ba kai min kmr auwal ba....., banason yaya al'ameen din nan wallahi..amman ummi kina neman takura rayuwarmu ..

"tunanin me kikeyi mueaddat kinyi shiru kina jina ?
 ahankali ta bud'e bakinta tace "babu komai ummi, tunda kin amince dashi, kin yarda na auresa ,naji na amince zan auresa kawai amman ina son ki min alfamar d'aya ummi?

ummi ta fad'ad'a murmushinta tana murna saboda jin dadi tace "wacce irin alfarma ce wannan mamana?
"ki fad'a min shi, ni kuma nayi miki alkwarin zan yi miki shi muddin bai fi karfina ba, idan bani dashi zan nemoshi matukar akwai shi acikin duniyar nan..

muwaddat ta numfasa ta runtse idanunta saboda d'acin abinda zata fad'a sannan tace " duk abinda za'a yi na aurena da yaya al'ameen har zuwa lokacin da komai za'a kankama , inason ayi shi a boye cikin sirri ummi...

 "ta yaya kike tunanin za'a yi maganar aure cikin sirri ?" waye bakyason yasan zakiyi aure?
muwaddat tayi shiru taki magana har sai da ummi ta sake maimaitawa, sannan tace"auwal .....
"ummi banason bunayya ya sani saboda banason yashiga damuwa "bakyason yasani saboda bakyason yashiga damuwa ?
ummi ta sake maimaitawa tana dubanta .
"bakyason yasani ko kema kina son kaninki kmr yadda yake naci ..?
 har zatace eh sai kuma tayi saurin girgiza mata kai ,"banason shi ummi amman kuma bazan so na gansa cikin damuwa ba ,ta k'arasa mgnr hawaye na ciccikowa a kwarnin idanunta "ummi tsakanina da Allah banason yaya al'ameen amman tunda kin yarda da natsuwa da nagartarshi

wallahi na amincewa zan aurensa ...
,nasan zan so shi daga baya....amman a halin yanzu gsky banason shi...

ummi tayi saurin kamo hannuta tace "anya kuwa yarinyar nan lafiyarki kalau?
"Anya kuwa muwaddat baki da aljannu kowa kice baki so ..?
" tun tasowarki kike samun masoya amman kowa yazo sai kin kawo aibunsa"
 "nifa bani da komai ummi kawai dai banasonsu ne ta k'arasa mgnr hawayen da take k'ok'arin makalewa suka samu nasarar zubowa..

"ummi tace ashsha abun har da kuka?
" to abar zance al'ameen din kawai tunda shima baki son shi, ta d'ago kanta tana duban ummi
"a'a ummi ni nace na amince wallahi zan auresa, kuma zanso shi saboda shima bashi da makusar da zan kisa.. ..
"to shikenan kukan ya isa haka Allah yayi miki albarka zan fad'awa abi sai ayi masa magana ya turo magabatansa .

"zance bunayya kuma ki ajiyeshi a gefe ,banason ki damu kanki saboda shi, shiyasa nake Allah Allah ya koma ,kuma nasan kafin ya dawo anyi komai angama, muwaddat bunayya ba sa'an aurenki bane, koda kina sonshi bazan bari ki auri kaninki ba azo Yana baki ciwon kai , bare baki sonshi , idan kuma kinsa kema kina sonshi ne sai ki fad'a min?

Jikinta na rawa ta girgiza mata kai , tana jin yadda bugun zuciyarta ke tsananta, ina ma zata iya fitowa ta fad'a wa ummi wallahi da tayi, domin babu wanda ya dace daita sai d'anta Muhammed auwal ...

sun rabu da ummi tana cikin damuwa mara misaltuwa, gabad'aya komai ya tsaya mata ta dinga jin kmr ana k'ok'arin rabata da rayuwarta ne ,amman haka ta dinga d'aurewa saboda kar ummi ta fahimci maganar ce ta haifar mata da damuwa ...

Tunda asirinsu yaso tunowa muwadda ta kiyayi kanta dashi ta daina sakar Masa fuska bugu da Kari Kuma zance al'ameen da kullun ummi take damunta dashi ,yasa take sake nisanta kanta dashi.

abu fa kamar wasa zazzabi dare ya saka muwaddat gaba kullun daren da zazzabi take kwana, ga amai kmr zata amayar da hanjin cikinta ,
 yau dai bunayya ya kawo mata ziyara sbd ya kasa hakuri , yanayin jikinta yayi matukar firgitashi ,har ya mike zai koma part dinsa ya d'auko kayan aikinsa Dan ya dubata, sai kuma ya kasa barinta ya koma ya kwanta a bayanta ya zagaye kugunta da dukka hannunwansa da zumar washegari zai dubata special ya gano takaimai mai matsalarta

****
washegari bayan ya tabbatar da ummi tana gurin duba percent dinta, ya had'a ruwan allurar da

zai yi mata ya nufi makarantasu, ya kirata a waya tun daga nesa ya hangota tana taku anatse tana yauki kamar batason taka kasa abinda ke mugun burgeshi daita kenan yanga da shagwa'ba, gashi tattara komai da duk wani cikaken lafiyayyen nmj ke so ajikin mace, tana sanye cikin riga da siket sai abayar data d'aura akansu da mayafin abayar data lullu'be kanta, amman hkn bai hana koina ajikinta motsawa ba, idan tana tafiya dole duk wani lafiyayen namji ya ganta ya kyasa, had'e da Mata kallon na musamman , idan kaga yadda take taka kasa kuwa zaka d'auka da ganga take juya jikinta amman kwata kwata ita kanta batasan ma tanayi ba.

tayi matukar yi masa kyau yana kallon mutanen data gifta sun kasa d'auke idanunsu akanta saboda amsa sunanta na cikakkiyar mace, tana rike da wasu takardu sai wata jaka data rataya a kafad'arta, dayan hanunta kuma waya ce mai dan karen tsaida ahankali ta k'araso jikin motarsa wanda shi tuni kishi yasa shi runtsen idanunsa, ahankali yake jin yadda yanayinsa ke sauyawa akanta, bai bud'esu ba sai dayaji tana kwankwasa glas din motar ,sannan ya bud'e idanunsa da kyar ya bud'e mata murfin matar tashigo ta zauna ,ya kai hannunsa ya ta'ba jikinta yaji babu zafi kmr daren jiya, ya sauke sanyayyen ajiyar zuciya "kinci abinci ne?
ta girgiza masa kai kawai "yanzu yaza'ayi Kennan magani zanbaki ?
" kabani kawai tayi mgnr atakaice" bazai yiwu nayi na baki ci komai ba " yasoma k'ok'arin tada motar, ba tace masa komai ba ,har suka bar harabar makarantar wani had'ad'den gidan abinci ya kaita yace "fito muje kici abinci "kaje kawai ka siyo ka kawo min nan idan nashiga bazan iya ci ba ...
"yayi shiru kamar zaiyi magana sai kuma ya share yashiga ko cikakken minti goma bai yi ba ya fito hannunsa rike da farar leda ya bud'e motar ya shiga ya bud'e farar ledar abinci , ya fito da roba dake d'auke da jallof da fridrice a had'e da nama kaza, da salad da gabeje tana ganin abincin miyonta ya tsinke jikinta har rawa yake ta amsa tayi gefe da sallad din tasoma ci hannu baka hannu kwarya abun har yaso bashi mamaki, yayi shiru kawai yana kallonta taci sosai ya bud'e kwalin hollandia ya mika mata ta amsa tasha har da ruwan
batare da 'bata lokaci ba ya kamo hannuta " me zaka min ta fad'a tana yatsina fuska, kasan fa ni banason wannan abar magani kace zakabani na sha ....
yayi kasa da muryarsa sosai yace "kiyi hkr nayi miki allura nan saboda yawon zazzabin da kikeyi ya dameni , nasan halinki bazaki ta'bawa fad'awa ummi ba ,kinga ita kuma bazata san halin da kike ciki da daddare ba, sai ni yayi mgnr yana narke mata ajiki had'e da buso Mata iskar bakinsa....
ya cigaba da magana a raunane saboda yasan ba magana zatayi ba
"idan na tafi na barki cikin wannan halin, hankalina bazai kwanta ba baby "ko kin fi son na tafi cikin tashin hankali ?
ta girma masa kai" okay to ki bari nayi miki allura har gwaji na musamman nake son nai Miki amman nasan bazaki bari ba , ta runtse idanunta gam dan kar taga lokacin da zai mata allurar, ahankali ya tsaita jijiyar hannunta ya tsira mata allura har guda biyu sannan ya ja motar ganin ba hanyar makaranta ya d'auka tace " ina km zaka kaini ?
"S. T hospital...
"No ka maidani makaranta kawai .. babu yadda yadda yadda iya haka ya maudaita, tsukayi sallama , ya tafi , byn ya gama kissing dinta , duk yadda taso ta gujewa bunayya hk ya gagara

tana ji tana gani ya sake dawo daita ruwa tsundun ?

ana gobe jirginsa zai d'aga suna kwance cikin bargo suna manne da juna, wanda a duk sanda suka kasance , haka suke d'auka kansu tamkar su din ma'aurata ne, ta kan mance komai da kowa har ma da matsayinsa garesa , bunayya yashige jikinta sosai yana magana kasa kasa "dan Allah muwaddat kada ki rabu dani ina sonki ki rikeni amana idan kika rabu dani mutuwa zanyi, dan bazan juri zama acikin duniyar nan ba babu ke, kada ki juya min baya, kada ki kula kowa...
ki jirani naje na k'arasa karatuna shekara biyu ne kawai nasan lokacin su ummi zasu aura min ke ,karki aure kowa , karki saurari wancan wawan da.. d'ayan hannuta tasa ta toshe masa baki ,shi kuma yashiga romacing dinta daman kuma babu kaya ajikinsu haka sukayita rud'a juna har dai ya biya bukatarsa daita. ....

****
daren ranar da bunayya zai bar kasar kuwa, muwaddat ji tayi tamkar karsu rabu da juna , suna makale da juna a d'akinta sai wani ririta juna suke,yayinda bunayya ke d'aukar mata alkawarurruka iri iri amman ita ko sau d'aya batayi kuskuren d'aukar masa alkawari ba saboda tasan koda tayi hakan ba cika masa zatayi ba .

tuna wannan dalilin yasa hawaye ya cicciko acikin kwarnin idanuta , har yasoma gangarowa bisa kuncinta, dumin saukar hawayen yaji a chest din'sa ,yasa shi d'ago fuskarta, amman still baya ganin komai saboda hasken da bai gama gauraye d'akin ba, dan hk yashiga lalu'ben makunnin wutar d'akin ya kunna, ya tsura mata tsumammun idanunsa yana kallonta cike da matsanancin so...

bai yi mamakin ganin yadda take zubar da hawayenta ba, saboda yasan shakuwarsu ta zarta haka, Nan take bunayya yashiga goge mata hawayen yace "ki daina kuka nan, banason kina min hasarar hawayenki, duka abun bana kuka bane ai "zan "dawo gareki nan bada jimawa ba ...

"ni dai ki rikeni amana bazan gaji da furta miki wannan kalmar ba, kece karfin gwiwana muwaddat ,nasan idan kika tsaya min, duk ta ummi mai sauki ne, sannan muddin kika fito kika sanarwa ummi cewar kina sona nasan zata yarda ta amince ta barmu mu auri juna tunda tana son farincikinki..

wasu sabbin hawaye ne suka sake ziraro mata saboda tasan har abada bazata iya ba.....
"bazata iya fuskantarwa ummi wannan zance ba, duk da yadda take matsanacin kaunarsa ta gwamaci ta dangwama a haka matukar sai ta bud'e bakinta ta furtawa ummi cewar shi take so,tana makale dashi ajikinta suna faranta ran juna da tsuma zuciyoyinsu da salon soyayyarasu ,sai kusan asuba suka rabu da juna.

washegari da safe da zazzabi dukansu suka tashi ,sai dai nashi bai nuna ba ,sai daya gama shirinsa cikin wasu hadd'aun kananan kaya wad'anda suka amshi jikinsa, sai kamshi daddan turarensa yake xubawa ,kyawawan idanunsa wanda suka wadatu da gashin kamar yadda

girarsa take suka sake fito da ainihin kyawun halittar da allah yayi masa ,agogonsa na rolex ya d'auko ya d'aura a tsintsiyar hannunsa ya gyara sumar kanshi da yake mugun kashewa kudi ,ya tsaya yana karewa d'akin nasa kallo ko baiyi mantuwa ba ...

koda ya fito shad'aya daidai ya nufi part din iyayensa bakinsa d'auke da sallama yashiga, suna zaune a parlour'n su duka har muwaddat wace ko kallon inda yake batayi ba ,shi kuwa tunda ya shigo idanunsa akanta suke, ahankali ta sauke boyayyiyar ajiyar zuciya amman ta kasa d'ago kanta ta kalleshi.

ahankali ya dinga aika mata da wani sihitaccen kallo na gefen idanu, sai daya gama kare mata kallo tsab sannan ya maida kansa gurin iyayensa yana masu sallama .
jikinta a matukar sanyaye ta yunkura zata tashi ,ya ji tamkar ya dakatar daita ya cigaba da kallonta saboda baya gajiya da kallonta zai iya bata tsawon lokaci akanta , duk wani jin kai tattare da miskilancinsa baya tasiri akanta, ita din daban take acikin duniyarsa ,sannan kadara ce mai tsaida wanda bai san yadda zai misalta tsadarta ba, agurinsa, a sukwane ya bita da kallon so har sai da ta kusan 'bacewa ganinsa .

sautin muryar abi ne yayi saurin dawowa dashi cikin hankalinsa, ya lumshe tsumammun idanunshi yana kallonsu gabad'aya , abi yasoma mgn cikin harshensa mai taushi wanda ke nuni da nasiha "bunayya.....
" na baka amanar kanka da rayuwarka, kasan kai kad'ai nake da ,duk duniya banida wani gudan jini sama da kai wannan kasar da zaka babu mu kaji tsoron allah akan duk abinda kazayi ,sannan abu mafi mahimmanci ibada ... ..
ya k'arasawa mahaifinsa nasihar daya saba yi masa a duk sanda zai bar kasar.
daga ummi har abi dariya suka kwashe dashi sosai ,ummi tace "shiryayye wato ba zaka barsa ya fad'a ba ko?

"to ummi idan dai ni din ba kwalkwaluwar kifi gareni ba ,yaci ace na haddace wannan nasihar ta abi, sosai sukayi masa fad'a da nasiha daga karshe abi yace "burinka ya kusan cika domin kana hada Master's dinka the nest thing aure zan maka "
ya matso da sauri kusa da abi dan bai son ummi taji ,yayiwa abi rad'a acikin kunne.
 ummi tace "ka gama fad'a masa abinda zaka fad'a
 nasan ina zaune zanji daga baya ,dan hk mai zai dameni.

murmushi bunayya yayi yace "ai ba wani abu nace masa ba, cewa nayi idan na had'a Master's dina zai aura min muwaddat?

wannan ne kuma ba'a Isa ba ,yaro karyarka tasha karya muwaddat tayi maka girma.....
 ya shagwa'be fuska "kai ummi ni wallahi bata wani min girma ba dan ko a yanxu kuka bani ita shikenan na samu mai debe min kewa ,amman tun da kun hanani a sauka lafiya nima banaso yanxu "kar ka sota mana mai diyata zatayi da kai k'aramin yaro da kai ..

"wannan ba gsky bane ai kuwa babana bashi da makusa ,sai dai ta shekaru inji cewar abi suka sake fashewa da dariya har sanda suka fito harabar gidan suna barkwanci amman bai ga al'amun muwaddat na da niyyar fitowa suyi sallama dashi ba, yaji kamar ya koma yaje ya sameta sai dai ya share,ya k'araso ya rungume ummi ajikinsa itama ta rungume shi had'e da kamo fuskarsa ta sumbaci goshinsa "allah ya tsare min kai abinda aka tafi dominsa Allah yasa asamu allah yayi maka albarka daga can kasamomin kyakyawar suruka yayi murmushi kawai ,ummi da kanta ta bud'e masa mota yashiga gidan baya ya zauna ,abi ma yashiga direba ya tayar da motar yana d'agawa umminsa hannu ,itama hannu take daga masa, tana tsaye har sai dataga fitarsu. ..

akan hanyarsu ta zuwa airport bunayya ya juyo ahankali tare da kamo hannu abi cikin nasa "i have to talk again abi, i really has to this before everything could mess up wit us .., bazan gaji da furta muku cewar muwaddat nake so va ....
And banzan iya cire soyayyarta araina ba .. ni kaina bansan lokacin dana kamu da matsanancin soyayyarta bare nayi tunanin cirewa i just has to dash the love out sbd bazan iya rayuwa babu ita ba.

"bunayya kayi kankanta da aure, as age of 22 year's, karatu ne yafi dacewa da rayuwarka ba aure ba a halin yanzu ,banci a wata kasa kayi karatunka da yanzu baka taka wannan matsayin da kake ba, ballanatana har kayi zance aure , bama haka Ba ,kabi umarni mahaifiyarka tukuna ,tunda ta nuna bata son aurinka da muwaddat .....
Bunayya ya d'an lumshe idanunshi kad'an ya bud'e yace "me yasa abi?
"me yasa kai ma kake son biyewa ummi?

"abi kai nmj ne ka fuskanci maganata da kyau, idan nashiga wani hali a sanadin wannan damuwar kusani kune sanadi, sam bani da muradin aikata zina arayuwata amman...

"amman me?
"kana nufin zaka aikata zina kenan akan wannan maganar ?

Bunayya ya girgiza masa kansa dan bai san abinda zai sake fad'awa abi ya fahimcesa ba, dan haka yayi shiru ya kasa magana, bangaren abi gabad'aya ya kasa kwakwaran motsi ,dan maganganun d'ansa sun sanyaya masa jiki,sai dai akoda yaushe yana mamakin yadda bunayya yake nuna maitar son aure a zahiri.. .

"duk nawa yake a idanunya ?
"yaushe aka haifeshi ya girma har da zai dinga kwadayin son aure hk ?
shi dayake son ya zama cikakken namiji sannan tsayayye wanda zai dogara da kansa ko bayan baya raye?

yasani kowane daga ciki yana da amfani aure da karatu amman shi a son ransa baya son yana zance aure yanzu ,yafi son yagama karatunsa gabad'aya.
Shiru bunayya yayi ya rafka tagumi cikin zullumin da rashin sanin madafar tunaninsa, abin

daya sani yana matsananci kaunar muwaddat kuma baya jin duk duniya akwai wanda ya isa ya raba tsakaninsu, har suka isa airpot tunani bai barsa ya huta ba..

da kyar yasamu ya fito daga cikin motar direba yayi saurin bud'e boot ya ciro karamar akwati kayansa yana mika masa dan daga inda suke ko taku daya basu kara ba ,ahankali ya kai hannunsa ya rike akwatin ya isa gaban abi sukayi sallama cikin sauri dan har an fara kiran mutane yasoma tafiya yana dagawa abi hannu shima yana d'aga masa sai kuma jikin abi yayi sanyi tausayin d'ansa ya kamasa, he really has to carryover everything in his life before everything could have mess kmr yadda ya fad'a Masa yanzu ..

Mmn sudais
2/7/20, 8:55 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

warning!!!

" don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

Wannan labarin na kudi ne

page 34

..jikin abi a matukar sanyaye ya koma gida, zuciyarsa a cunkushe , gabad'aya ya rasa abinda ke masa dadi arayuwarsa ,ji yayi tamkar zai rasa tilon d'ansa ne a wannan karon sakamakon bugawar da zuciyarsa ke yi , shiru yayi yana kai kawo acikin d'akinsa yana dogon tunanin akan lamarin bunayya "Ina sonka ya kai d'ana .....
"Ina son ka rayu cikin farinciki ....
"Bazanaso ganinka cikin tashin hankali da damuwa ba ..
"Tabbass lokaci yayi da zan yi komai akan son zuciyarmu , matukar ina raye duk runtse duk wuya muwaddat ba zata su'buce mana ba.. .....

Cikin wannan halin ummi tashigo d'akin ta riske shi , ai ganinsa tsaye cikin wannan tashin hankalin , yasa ta k'araso da sauri tana kallonsa a firgice.
" hubbey me yayi zafi haka ?
"meke damunka ? Tayi Masa tambyr ajere, hankalinta a matukar tashe ta kamo hannuwansa duka cikin nata suka zauna atare agefen gadonsa tana kai hannunta fuskarshi "ka sanar dani damuwarka mijina.....

Muryarsa a raunane yace "bunayya .....
sai Kuma yayi shiru ya kasa k'arasa maganar "me kuma ya samu bunayya da yanzu kuka rabu dashi ?
"Hubbey bunayya na cikin tashin hankali ,bunayya ya bar kasar nan da muradin mallakar muwaddat arayuwanshi "bunayya na matukar son muwaddat fiyye da tunaninmu...
" yakamata ki duba wannan a'lamarin plz..bugu da K'ari Ina jin tsoron abinda zai faru dashi ,ya tafi cikin tsananin tashin hankalin da bazan iya misalta miki ba , bunayya ya tafi ya bar zuciyata cikin damuwa, Ina ji tmkr na dawo da d'ana gareni nayi masa abinda yake muradi .....

Naunayen ajiyar zuciya ummi ta sauke "yanzu akan wannan mgnr kawai zaka saka zuciyarka cikin damuwar ?
"Ba akan wannan maganar kawai bane ..."
"Wannan maganar ta wuce akirata da kawai ,idan kawai ce agurinki ni agurina ba kawai bace ..
" Domin bunayya ya cancaci fiyye da haka agurina ...
shine komai na rayuwata, shine duniyarta , yau idan bana raye shine majibancin alamarana , ta yaya kike tunanin bazan damu da damuwarsa ba ..?
"Dole na damu damuwarsa , idan son samu ne ma muyi masa abinda ya bukata daga garemu ..
Ummi taja dagon numfashi ta fesar ahankali tace "yanzu nufinka ayi masa aure ko me kake

nufi ?

"Exactly abinda nake nufi kenan ,tunda ya nuna yana son aure , ni Kuma inshallahu zan yi masa ,idan ma baki bada had'in kan da zai auri muwaddat ba, zan aura masa diya ko ta uban waye tunda nasan d'ana bashi da wata mummunar kama ko mugun halin da za'aki bashi aure.... ya k'arasa mgnr cikin fushi yana zare yatsunsa cikin nata , abinda bata ta'ba gani ba kenan a tun tsawon rayuwar aurensu .....

"Wai fushin ishaq yayi daita akan d'ansa ko me ?
" 'lallai wannan abun mai girma ne a zuciyarsa ..
Shiru tayi tana dubansa tana nazarinsa ahankali ," tunda shi yayi fushi a halin yanzu, ita bai kamata tayi ba, dan haka cike da mutuwar jiki ta sake kamo hannuwansa tace "kayi hakuri dan Allah , na fuskanci kmr ranka ya 'baci sosai akan matsalar nan ,kada zuciyarka tayi wani tunani akaina ni.. ....
"Kema me ..? Ya katseta ta hanyar fad'ar haka yana huci .
"Ta Yaya kike expecting zuciyata bazatayi tunani akanki ba ?
"Idan zaki amince ki amince ki Sanya hannu ayi komai, Banga dalilin da zai saka ki dinga yi masa kallon yaro ba alhalin yaro ya nuna mana cewar shi ba yaro bane ..
"Akwai wad'an da Basu kai bunayya a komai ba,Kuma anyi musu aure har ma su haihu bare shi..."

"shikenan naji but ka kwantar da hankalinka dan Allah, ka saurareni "nima bawai bana son yayi auren bane, zan fi kowa son haka atsakaninsu ,"wallahi tallahi ina son bunayya da muwaddat amman ka duba lamarin nan hubbey ka gani ,mai bunayya zai iya yi muwaddah a fanni auratayya bare aje ga zaman kewar rayuwar zaman aure ?
" Bana tunanin zai iya mata wani....
"ki bashi ita mana ki gani ko zai iya ko bazai iya ba..
"idan zaki canza tunaninki ki canza ni dai na rigada na gama maganata , zan tuntu'bi muwaddat akan shi matukar ta nuna tana son shi ,zan aika masa da ita can sun karata .. ya k'arasa mgnr Yana Mikewa tsaye cikin tashin hankali....
Itama ta mike tsaye tana cigaba da dubanshi "zaka aika masa da ita fa kace ?
Yace "yes of course"
" Sai kace wata kaza "to ai baby bata so shi bare ka aika masa ita wata uwa duniya.. ,"kama cire wannan son zuciyar naka akan d'anka , dan zance da nake maka ma yanzu tuni muwaddat sun gama magana da al'ameen akan zai turo iyayensa ...

abi yayi shiru zuciyarsa na dokawa "sun gama magana da wa kenan ..?
"da al'ameen mana..ta bashi amsa tana tsare shi da idanuwanta. "yakamata mu cire son zuciya acikin lamarin nan , a zahirin gsky idan zamu bada auren muwaddat mu bawa Wanda ya girmemeta, ba wanda ta girma ba, tunda shi aure ba wasan yara bane ....
Ahankali yasoma taku had'e da Juya mata baya ya cikin kunar rai, yana fuskarta window d'akin..
Itama ummi cikin fushi ta bar d'akin ta nufi d'akinta ....

Ummi na barin d'akin ,abi ya d'auki wayarsa yasoma neman layin uncle umar kaninsa ,Kira d'aya biyu , uncle umar ya d'auka had'e da yi masa sallama"assalamu alaikum"
daga can bangaren abi naji ya d'auka ya amsa masa da "waalaikum Salam, kana yace "umar sabuwar matsala fa taso a gidana gabad'aya ban San yadda zanyi ba " nan abi yashiga zayyanowa uncle umar komai tun daga zuwan bunayya har zuwa yau din nan daya bar kasar . Uncle umar yace "karka damu Yaya wannan bawata matsala bace , komai zai zo da sauki inshallahu ,ka bari zan Kira ita ummi na fahimtar daita nasan zata fahimta ,"wace irin fahimtarwa zakayi mata ?
" Zaka mata bayani komai ne, sbd lamarin fa yasoma fin karfina ?
"to me ka gani a fad'a mata ne ?
"zan so haka gsky dan...
"No Yaya kusan fa ummi ta fika gsky ta wannan bangaren, karka biye bunayya plz ,da akwai kuruciya acikin lamarinsa, idan ma hakan ce zata kasance abarshi zuwa gaba plz ,tautauna suka cigaba da yi akan lamarin kafin daga baya
sukayi , sallama .

Bunayya na sauka a kasar london muwaddat ya soma kira amman number's dinra shiru basa shiga, dan haka ya kira na ummi,batare da 'Bata lokaci ba , ta d'auka suka gaishe muryarta a kausashe mai nuna al'amun tana cikin damuwa yace ,"umminah me ya sameki naji muryarki somehow like kina cikin damuwa ?
"Babu komai ya ka Isa ?
Muryarsa a sanyaye ya sheida mata ya sauka lafiya ta gayawa abi.. .. sukayi sallama, ranar dai duka ahlin gidan yini sukayi cikin damuwa ,most especial abi wanda ya fi ummi d'aukar zafi, dan ko lokacin dataje d'akinsa yaki sakar mata fuska, bare wani rawar jiki daya sabayi akanta amman dayake tasan ta kan kayanta haka ta dinga binsa da rarrashi da dadin baki da komai har dai ta d'an shawo kansa suka daidaita ..

****

tunda bunayya ya bar kasar take cikin damuwa da tashin hankali gabad'aya ta fita haiyacinta, kallo d'aya zaka mata kasan bata cikin natsuwarta da kwanciyar hankalinta, komai dai yinsa take dan kar ummi ta harbo jirginta ....

Duk wunin yau babu inda ta leka ko makaranta bataje ba saboda zazzabi daya rufeta, da taimakon ummi ta dawo normal , sai dai ummi haka nan take yiwa muwaddat din wani irin kallo na daban,zuciyarta nayi mata aiyane aiyane akanta ,lokacin datayi tunanin danganata da asibiti domin duba cikakken lafiyarta ,sukayi gari muwaddat din tana murkususun ciwon mara ,d'aga karshe sai ga jini ya barke mata , wannan Abu ya kwantar da hankalinta ummi sosai ta sake bata magani da allura , bayan kwana uku muwaddat ta d'an samu sauki dan haka ta shirya zuwa makaranta ,ummi na ajiyeta tashiga cikin makaranta ta isa deptment dinsu , ko

minti goma batayi ba sai gasu fatima da zainab kawayenta suka shigo , da sauri suka k'araso gurinta fatima tace "muwaddat lafiya kwana biyu baki zo makaranta ba?

muwaddat ta yatsina fuska tace "kema kinsan duk abinda ya hanani zuwa makaranta koda rana d'aya ne, abu ne mai mahimmancin gaske , ballantana har kwana uku.
  "ikon Allah to me ya faru wallahi hankalinmu yayi mugun tashi har fa muna tunanin zuwa gidanku?

muwaddat ta tsuke k'aramin bakinta tace "rashin lafiya ce amman yanxu naji sauki sosai "suka had'a baki gurin mata "Allah ya sauwake sannan suka shiga duba hand out dinsu..

bayan sati biyu al'ameen ya kirata bayan sun gaisa yayita mata hira, tun tana basar dashi har da tasoma amsa shi sama sama daga karshe yace mata yana son cikin weekend din nan "zaizo ko kar yazo?
 tace masa "babu komai kana iya zuwa ,yaji dadi sosai .

muwaddat tana gida kasancewar weekend ce, bata zuwa makaranta tana ta harkokin gabanta sai a lokacin ta fad'awa ummi zuwan al'ameen,ummi tace allah ya kawoshi lafiya ,ai bakiji yadda nake son yaron nan ba, irin mijin da nake miki fatar samu kenan cikakken namiji mai zati da haiba "wannan idan kika aureshi zai ririraki saboda yana da sanyi hali .

  jikin muwaddat yayi sanyi ,da jin abinda ummi ta fad'a yayinda lokaci lokaci gabanta na faduwa musamman idan ta tuno bunayya , duk sanda za suyi waya dashi maganarsa bata wuce ta rike shi amana ta jirasa har sanda zai dawo .... .

bayan ta gama breakfast ta shiga bayi tayi wanka, farar hoda kawai ta shafa saboda batason kamshin man shafawarta yanzu , tashiga cikin wata hadaddiyar koriyar doguwar riga gashinta ta jima tana gyara shi saboda tsawonsa da tsantsi ta fashe jikinta da turare mai sanyi kamshi tare da k'ok'arin dasa digon kaunar al'ameen aranta, tunda yana neman ya zame mata karfen kafa, ta fito parlour ta d'auki litaffin karatunta tana dubawa kafin ya k'araso , bata fi minti biyar da zama ba sai ga kiransa yashigo, ta dubi ummi kawai ,itama ummi kallonta tayi tace "halan ya karaso ne ?
"bansani ba"
" to ki d'auka kiji ko ya karaso ne?

ta d'auka had'e da mikewa ta bar gurin dan bazata iya amsa waya a gaban ummi ba,byn minti biyu ta dawo tace "ashe wai har ya karaso ,"to maza shirya ki tafi sai ki kai shi parlour'n baki "

ahankali tabi ta cikin main parlour'n ta shiga parlour'n baki ta bud'e ta waje tare da lekawa farfajiyar gidan , aiko dashi idanunta suka soma cin karo, suka had'a ido dashi yana jingine jikin motarsa ya hard'e kafafunsa, sanye cikin wata had'ad'diyar shadda dinki jamfa idanunsa manne da glss Yana kallonta , kusan minti goma idanunsa na kanta ya kasa d'aukesu " ta d'an lumshe idanunta , ahankali yasoma

ta kowa ta matsa baya kadan domin bashi hanta ,,shi kuma karasa har cikin parlour'n, ta biyoshi abaya tana nuna masa gurin zama ya zauna idanunsa akanta ,ahankali ta motsa labbanta tace "ya gajiyar hanya ?

yayi murmushi yace "ai babu wata gajiya, idan ma akwaita babu ita yanzu tunda na ganki , tayi murmushin nan nata mai tafiyar da ruhi, tace "to dame zaka soma abinci ko kayan motsa?
" tukunan dai"

 "tsiyaya min lemu kawai ya isheni ,inta kallonki , kallonki kad'ai ya isheni, ta kai hanuta ta tsiyaya masa lemu a glas cup ta mika masa ya amsa yana had'awa da yatsun hannunta ,take jikinta ya kama rawa ganin haka yasa ya amshi cup din ya sha kad'an ,ya ajiye tare da kiran sunanta "muwaddat kina da matsayi mai girma agurina ban ta'ba cewa ina son wata mace arayuwata ba sai ke, dan Allah ki soni koda ba zai kai kwatankwacin wanda nake miki ba ,ina rokon wannan alfarma, babban misali shine yadda na taso tun daga ilori zuwa lagos dan na ganki , ina neman yarda daga gareki zaki aureni ?
mayafin doguwar rigarta tasa ta rufe idanunta dashi amman ta kasa amsa masa ..
dadi ya sake rufeshi domin hango nasarori acikin wannan had'uwar tasu ba kamar sauran lokutan baya ba ,duk inda aka samu kunya to soyayya na nan, koda babu yawa al'ameen bai cika son ganin mace cikin shigarta irin wanda ke jikin muwaddat ba a yanzu, burgeshi da mace tayi shigar riga da siket ko duk wasu kaya da zasu dame mace jiki su fidda surarta a sarari ya kalla yadda yaga dama .

wannan kayan da suke jikin muwaddat bazasu bashi damar ganin komai nata ba sai kyakkyawar fuskarta amman akanta yazamota shigar na matukar burgeshi komai nata yazamo da ban acikin mata kullun zaka ganta cikin abaya take amman hkn bai hana surarta bayyana .

ahankali ya taso daga mazauninsa ya dawo daf daita ya zauna" duk abinda yakamata na fad'a na rigada na fad'a ta bakinki kawai nake jira

tayi shiru na kusan minti biyar daga bisani ta numfasa tace "yaya al'ameen...
  ya tsura mata ido yana kallonta cike da fargaban abinda zatace, allah kadai yasan halin da zuciyarsa ta shiga alokacin data ambaci sunansa , ta cigaba da magana cikin sanyi murya "zan fad'a maka wata magana guda daya yayi saurin katseta "dan allah idan kinsan bazata faranta min rai ba, ki bar maganar domin ni yanxu abinda zai sanyaya min rai nake bukata daga gareki idan kina sona kawai kice kina sona muwadda a wuce gurin .

tayi murmushi kawai saboda gani yadda gbdy ya rikice, yace "bakya sona ko muwaddat .. ?

"gaskiyar magana yaya al'ameen zance ace ba'a sonka ma bai taso ba ,baka d'aya daga cikin mazan da diya mace zata ki ko wace ce ita kuwa "to meyasa kike kunbiya kunbiya akaina ?

tace ba kunbiya kunbiya bane yaya al'ameen ina da dalilina mai karfi ya saukar da kwayar

idanunsa kasa yana jan numfashi da kyar "wani irin so yake mata mai zafi hk? Ya tambayi kansa.

cikin haka wayarta tashiga Kara ,ahankali ya kai ganinsa kanta daga inda yake yana iya hangon mai kiranta amman sunan kanina daya gani ne a rubuce yasa shi sauke naunauyen ajiyar zuciya "muwaddat ki bari muyi magana kune da kune umminki da kanta ta kirani ta bani umarni zuwa, nasan tayi magana dake kafin naxo idan kinsa bakya sona ki fad'a min sai na hakura saboda banason takurawa rayuwatarki.

"ita ba wai kalmar so bane bazata iya fad'a ba, shi din ne ba zata iya fad'awa ba, gara kawai ta amince da zata aureshi akan ya tutseyeta akan tana son shi ko bata sonshi, bunayya nata faman kiranta amman taki d'aukar wayar daga karshe ma ta jawo wayar ta kasheta gabad'aya, ya sake numfasawa "to zaki aure ne na turo magabatana a saida mamaga mai karfi ..?
ya furta mata wannan kalmar yana tsareta da idanunsa, ahankali ta daga masa kai "yayi murmushi kawai "shikenan nagode yasan tabbas batason shi amman bazata iya furta masa hakan ba, koma dai yaya ne ,tunda ta amince bazai yi sanya agwiwa ba, ahankali yashiga janta da how, wata maganar ta bashi amsa wata tayi shiru da zai tafi ya tursasata sai tayi masa rakiya gurin motarsa tana tsaye ya bud'e motar ya fito da manya fararen lododi guda biyu duk shake da kayan ciye ciye, duk abinda yasan tana so sai daya siyo mata har ma da wanda bai sani ba, kudi ne dai bai bata ba, dan yasan koda ya bata bazata amsa ba..

har dare muwaddat ta kasa kunna wayarta saboda matsanacin tsoron tuhumar da bunayya zai yi ,yanzu idan ta kunna ya kirata mai za tace masa?

shi kuwa har wannan lokacin nemanta yake a ways bai samu ba, gashi yana son ya kira ummi yaji ko lfy sbd zuciyarsa bata ta'ba shiga damuwa ba irin wannan lokacin, amman Yana fargaban kiran ummi , yana kwance bisa lafiyayen gadonsa rike da waya , ac dake manne da gadonsa yana aiki kmr me ,Amman sam damuwar da yake ciki yasa bai jin aikinta ajikinsa , ya kai hannu ya danna wani abu ajikin gadon domin k'ara karfin ac d'akin, babu abinda yake kaunar ji a halin dayake ciki kmr muryar muwaddat , domin jin muryarta kad'ai ya shafe duk muryar wata diya mace a zuciyarsa ,abin mamaki wai yau shine saboda jin murya mace ya shiga halin tashin hankali da matsanancin damuwa," a she haka yammata da suke rud'ewa akansa da son jin muryarsa suke ji idan bai d'auki wayarsu ba?

a wasu lokunta ma yana sane yake kin d'aukar wayar ko ya kashe ko yasasu a derveting, , ya kasa runtse idanunsa gashi dai bacci yake ji amman ina bacci yace bai san haka ba, ranar kwana zaune yayi yana neman layinta .

bangaren muwaddat tunda tayi sallar asuba ta koma ta kwanta ,sai gurin karfe goma ummi tazo ta tasheta taci abinci , byn ta tashi tayi wanka taci abinci ,sai ta kunna wayarta ta koma ta kwanta .

wuraren karfi 12:00 taji wayar ta dameta da k'ara cikin magagin bacci ta dauko batare da ta

duba ba tace "waye.....?
shiru yayi kirjinsa na wani irin bugawa da matsanancin karfi yana jin da zai iya ,da kuka kawai zai sakar mata ko ya huta da radadin dayake ji"
jin shiru yasa ta cire wayar a kunneta ta duba, sunan data gani yasa ta dan bud'e idanunta dake lumshe sannan ta maida wayar a kunneta tace "bunayya..... .....
da kyar ya numfasa yace" ke bacci ma kike yi ko ?
" Ni Kuma kika barni kwanan zaune ..
"yanzu muwaddat kin kyauta min kenan?
"me yasa bakijin tausayina for god sake?
" tun jiya ina nemanki a waya baki d'auka ba at least daga baya sai ki nemi...

"kayi hakuri na. na.. sai kuma tayi shiru "me kika yi dayafini zama important agurinki tun fa dana dawo na rasa gane kanki da gindinki "nace kayi hakuri "zanyi hakuri ne kawai idan kin fad'a min abinda yasa baki d'auki wayata ba "
yayi shiru yana sauraronta ta numfasa "ni dai kayi hakuri kawai "saboda kinsa kin cutar dani ko?

"amman babu komai ki cigaba saboda kinga ina sonki ne ,but kisani shi soyayyar da nake miki bazai hanani gwada kunjina akanki ba, "yazamo karo na karshe da hakan zai faru.....
yana gama fad'ar haka ya katse kiran ta mike zaune tana dafe goshinta ..

bayan wata uku da
komawar bunayya London , ala'meen zaune agaban alhaji Muhammad mahaifin muwaddat ,Yana karanto Masa bayani akan Yana son auren muwaddat a wannan lokaci .

Alhaji Muhammud ya numfasa kana yace "naji dadin wannan batun naka aminu ,sai dai wani hanzari ba gudu ba muwaddat dai ....
Sai yayi shiru ya gagara karasa maganarsa yana mai runtse idanunsa ,kusan minti goma suna zaune a haka sannan ya cigaba da maganarsa a tsanake "abinda zan fad'a maka Aminu ka bar zance muwaddat saboda ina da dogon buri akanta ban tashi aurar daita yanzu ba ,amman ga faiza nan na baka aurenta ,ko yanzu ka tashi aure ka sanar min ,nayi maka alkwarin zan ajiye karatunta na aura maka ita...

Shiru ne ya ziyarci parlour'n ,yayinda gumi yashiga tsatsafowa ala'meen ta koina ajikinsa , gabad'aya jinsa ne ya nemi d'aukewa ..
Ya yunkura tamkr wani zararre yasoma k'ok'arin barin parlour cikin tashin hankali dady ya bi bayansa da kallo ,tunda yake bai furta abinda taji ya damesa ba sai yau..

kai tsaye al'ameen bangarensa ya nufa kmr wani mahaukacin sabon kamu , yana shiga yashiga Kira ummi byn ta d'auka ya zayyano mata yadda sukayi da dady ,ummi tace " Banda abunka ala'meen meye nayi wannan zance da dady ?
"Yaya ne zai aurar da muwaddat ko mu ?
Kawai idan ka tashi ka turo magabatanka nan gurinmu ,na tashi aurar da diyata ....

da wannan furucin yasamu karfin gwiwar ajikinsa dan haka batare da Bata lokaci ba ya turo iyayensa zuwa ga abi domin nema masa auren muwaddat me zai yi da wata faiza shi zuciyarsa muwaddat tagani take so ba faiza ba , kafin iyayen ala'meen suzo ,ummi bak'ara min fama ta Sha da abi ba kafin ya yarda yace" suzo"

Dady bashi da masaniya ala'meen yayi gaban kasa ya turo iyayensa ,bayan sun gaisa cikin fara'a da mutuntaka abi yayi shiru ya zubawa sarautar Allah ido ,Banda murna da farincikinki babu abinda iyayen ala'meen suke, amman Banda abi da yake jin kmr an d'aura Masa dutse ne bisa kirjinsa , duk safiyar ranar haka ya dinga ji fad'awar gaba ..
An kawo baki abinci iri iri da abun Sha ,da kayan marmari iri daban daban daga ummi ,byn sun gama cin abinci suka soma magana akan abinda ya kawosu, Basu tafi ba sai da aka saida magana mai karfi tsakani, inda iyayen ala'meen suka ce Nan da wata goma cif suke son ayi biki .....

mmn sudais
2/7/20, 9:35 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

warning!!!

" don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

Wannan labarin na kudi ne idan kana /kina bukatar karantawa ki tuntu'bi wannan number 08059623096 or 08032384602

page 35

.....shi dai abi duk abinda iyayen al'ameen suke tautaunawa akai na batun aure, kasa cewa komai yayi ,illa zuciyarsa dake wani irin harbawa da sauri , babu abinda yake tunani da fargaban a halin da yake ciki facce halin da tilon d'ansa zai shiga ,yasani bunayya zai shiga matsanancin tashin hankali idan ya riski wannan labarin ,koma ya nemi zaucewa saboda shi kansa ya lura da irin mahaukaci kaunar da yake wa muwaddat
,itama Kuma muwaddat din ya lura tana mugu mugun sonshi .

 gabad'aya acikin lamarin sai yaga duk kuskurensa ne ,da tun lokacin da bunayya ya nuna masa yana bukatar ya aura masa muwaddat, yayi wani Abu akai da yanzu da muwaddat din zai koma karatu a matsayin matarsa ...
 "to yanzu shi mai zai iya cewa Kuma ?
"Ya zabi son zuciyar matarsa ya hana d'ansa abinda yake kwakwar so, to idan wani Abu ya faru dashi a sadin haka wa gari ya waya ?

"Kanka ka cutar zuciyarsa ta bashi amsa da hakan ..
"Tabbass haka ne zan cuci kaina da d'ana, idan na rasashi wa zai zame min gurbinsa a wannan duniya?
Ya sake jefawa zuciyarsa wata tambayar yana duban iyayen al'ameen d'aya byn daya .
"Muwaddat ba diyar cikina bace amman ina jinta tmkr ni ne na kawota duniya ,sai duk da haka, ai gurbin ido ba Ido bane, idan na rasa d'ana, rayuwarta zata cigaba yi agidan mijinta , domin kiyayyar mace na wani d'an lokaci ne, baya tabbata muddin rai ,gara tun wuri nasan abun yi akan lamarin tun kafin abubuwa sugama rinca'be min .

 sanyayyiyar ajiyar zuciya ya sauke da karfin gaske lokacin da yaji iyayen al'ameen suna sake furta wata goma cif suke son a saka ranar auren ,shi kuwa inshallahu kafin lokacin zai tabbatarwa kansa muwaddat ta zamo mallakin bunayya ne da yarda Allah ,ba mallakin ala'meen ba , koda kuwa hakan zai zamo sanadiyar 'batawarsa da ummi zai gwamaci haka amman tabbas zai bawa d'ansa farinciki .....
 haka dai taron ya watse batare da abi ya wani saki jikinsa ba, baki na barin gidan ya d'auki

wayarsa ya Kira alhaji Muhammad ya zayyane masa komai daya faru , cike da matsanancin mamaki dady ya dinga saurararsa har sanda ya dasa aya kana ya furzar da wani numfashi mai zai fi a ransa yace "kenan ala'meen haka zai yi masa ?
"da fari ya saka shi ya zamo k'aramin mutun a gurin iyayen litafa ,yanzu Kuma yana shirin rukujewa masa burinsa akan muwaddat ,amman babu komai zai saka masa ido yaga iya gudun ruwansa.....

****
A ranar da aka sa ranar auren muwaddat, haka nan bunayya ya yini da zazzabi mai tsanani, zuciyarsa ta dinga tsinkewa tana harbawa ,duk motsin da yayi sai gabansa ya fad'i, gabad'aya zuciyarsa tayi masa nauyi da kunci, zafi kashi da kashi yake ji acikin zuciyarsa..
Gashi daman tun daya shigo kasar cikin damuwa yake hakan ya rasa sukuni , ramar da yayi tayi yawa sosai har ta fito fili, haka fuskarsa ta bayyana dukkan damuwar dake zuciyarsa .

suna zaune a gurin shakatawa shi da abokansa, gabad'ayansu suna tsananin tausayin halin da suke ganinsa ciki , suka zabga tagumi kowane daga cikinsu ya kasa magana.

Nabeel ne yayi karfin halin magana yace" m.a ya dace ka cire wannan damuwar aranka tunda kazo kasar nan baka bar zuciyarka ta huta ba,kullun cikin tunani kake,ka shafe damuwar dake cikin zuciyarka, domin suna nuni ne da yadda ka yiwa rayuwarka kyakkyawar fahimta.

saboda a yanayi na matsayinka da wayewarka da gantanka da isarka, da wahala ace kana irin wannan tunani. domin su wad'an nan abubuwa guda uku daka mallaka kyau kudi ilimi suna sa mutun yayi kowani irin girman kai suke sa mutun,mutun ya dinga jin kansa ishashen da babu wanda ya isa sai shi,shi ke sa mutun ya dinga jin babu abinda ya isa yazo ya dameshi saboda isarsa da takama ..

saboda haka ina mai jan hankalinka tunanin da kakeyi a wannan lokacin yayi yawa , ka bar zuciyarka ta hutu ka yarda da kowani rin kaddara samu ko rashi..
M. A yayi tsit kansa na kasa ,ya kasa cewa komai har sai da Nabeel yayi shiru sannan ya d'ago kai ya numfasa.

Nabeel gabad'aya naji zantuttuka ,kuma zanyi amfani dashi, ina son ku ta yani da addua duk kwanaki nan bana jin dadin zuciyata da gangar jikina, ji nake tamkar ana zarar raina, jikina na bani akwai abinda yake faruwa gida,ko Kuma yake Shirin faruwa da rayuwata , nayi waya gida kowa na lafiya ban sani ba ko boye min suke ..
"to kayi addu'a mana shine mafuta inji cewar nabeel, "Inshaallahu duk zamu tayaka da addua amman ka saki ranka plz..

****
tun daga lokacin da aka tsaida magana mai karfi tsakanin al'ameen da muwaddat shikenan al'ameen ya maida lagos tamkar ilori da ogbomosho duk weekend din duniya a lagos take yi

masa, ta bangaren muwaddat babu yabo babu fallasa ta kan d'an sakar masa fuska ,shi kansa al'ameen idan akace masa muwaddat bata sonshi a halin yanzu zaice karya ne , saboda irin kulawar da take bashi idan tazo.....

 wasa wasa bunaya ya kasa samun natsuwar zuciya duk da suna waya da chatting da muwaddat kmr yadda suka saba amman duk sanda ya runtsa idanunsa sai ya kasa bacci, gashi dai kowa ta bangarensa lafiya lau yake, dan babu wanda basa waya dashi har muwaddat bai ga wata al'amun akwai wani damuwa attare daita ba yafi tunanin dai damuwar iya kansa kawai ta tsaya kullun damuwarsa na sake karuwa ya rasa mai ke damunsa da rayuwarsa gabad'aya .

Haka nan ta bangaren faiza taki barinsa ya huta, kullun zata kirasahi a kalla sau goma , sai dai duk nacinta haka zata gaji ta hakura dan daidai rana d'aya bunayya bai yi tunanin d'aukar kiranta ba, dan bai San me take nufi dashi ba ,bayan ya fito ya bayyana mata abinda ke cikin ranshi .
Ta bangaren faiza kuwa babu abinda ke dawainiya daita sai zallar shaukinsa da farincikinki burinta ya kusan cika tunda Yaya al'ameen zai zamo miji ga muwaddat tasan tabbas bunayya zai zamo mallakinta ,ta d'auki tamarar zatayi komai idan dai zai zamo miji gareta ...

 Haka nan yau cikin bacci ya mike a matukar zumbure yana mai dafe daidai saitin zuciyarsa dake bugawa da karfi, nan fa gumi ya rufeshi ta koina ajikinsa, ahankali "yashiga furta kalmar inna lillahi wa inna ilaihi rajiun.. .

cikin haka kiran faiza yashigo wayarsa yana dubawa yaga itace Yaja dogon tsarki tare da furta another matsala kawai.....
 ya ajiye wayar yana gyara kwanciyarsa ,ita kuwa jin tayi kira ya kai sau goma sha bai da niyyar d'auka kamar koda yaushe yasa taji ranta ya 'baci , ta dinga jin tamkar ana diga mata dalma ne akan zuciyarta ,take zuciyarta ta harzuka tasoma tunanin abinda zata masa wanda tasan babu makawa zai nemita domin Karin bayani .

Shiru yayi kawai yana tunanin matakin da zai d'auka akanta yaji shigowar sako da kmr bazai duba ba sai dai yayi tunanin ko muwaddat ce,dan haka ya lalu'bo wayarsa sakon da idanunsa suka ci karo dashi ne yasa shi tashi zaune da sauri yana sake dafe daidai saitin zuciyarsa dake harbawa har wannan lokacin , da karfi ya furta "what..?
 "When ?

 Kana ya tsurawa sako ido yana sake karantawa yana sake maimaita kalmar Inna lillahi wa Inna lillahi raji'un ga abinda sakon ya kunsa"

slm a lokacin danake rubuto maka wannan sakon ina cikin matsananci farinciki da annashuwa ,ina maka albishir da kaima zaka rasa cikar burinka daka girma dashi, yadda bazan sameka ba, haka kaima ba zaka samu damar cika burinka, domin kuwa yau kimanin wata daya kenan da aka saka ranar auren aunty muwaddat da yaya al'ameen har ma da sadaki atsakani, wannan abu yayi min dadi ni faiza za'ayi to zero

cikin wani irin tashi hankali ya zabura ya mike yana sakin qara tare da cewa "ba dai muwaddat dina ba, muwaddat tawa ce ni kad'ai ,duk runtse duk wuya babu wanda ya isa ya aureta sai ni...
nan take jikinsa ya shiga rawa ,yasoma k'ok'arin kiran faiza tana kallo wayar na ruri ta saki wani shu"umin murmushi "ai nasan zaka kirani ,ni kuwa bazan d'auki kiranka ba ,kai ma kaji abinda mutane sukeji ,tana kallo wayar na cigaba da k'ara amman taki d'auka daga karshe ma ta kashe wayar gabad'aya tana dariyar mugunta .

Gajiyayi yasoma neman layin muwaddat domin jin gskyr lamari amman shiru bata d'auka ba, gashi dai wayar tana ringing , hankalinsa yayi mugu mugun tashi yasoma ganin double, ya dafe goshinsa da hannuwansa duka yashiga bin bagon d'akin ,can ya saki k'ara mai sauti sai ga abokansa guda biyu sun shigo d'akin a matukar razane sukayo kansa suna tambayarsa "lafiya M. A me yasameka?

yayi shiru kawai yana dubansu d'aya bayan daya tmkr wani zautacce,ya dungule hannunsa d'aya ya naushi iska Yana furta " imposble .....wani ya aure muwaddat bani ba, ya wucesu cikin sauri ya k'arasa gaban wardrobe dinsa ya bud'e saboda ya rasa me ya kamata ya fara yi ,akwatin kayansa ya janyo yashiga zuba kaya yana kiran waya "

sai lokaci suka fahimci abinda yasa ya fita haiyacinsa , suka matso kusa dashi suna tambayarsa "yanzu ina zaka haka da kake k'ok'arin had'a kaya?

"Nigeria ya basu amsa atakaice ....."plz M. A.. ..
"don't dont say anything to me dan ba fahimtarku zanyi ba, sai sai.. .. yayi shiru tare da cilla da wayar bai gama jin mai ake fad'a masa acikin wayar ba .....

"haba M. A kayi hakuri mana kasanyawa zuciyarka natsuwa ,karka tafi cikin wannan tashin hankali ,Dan girman Allah ka bari zuwa ..."NO bazan bari ba sadik yayi maganar yana d'aga murya ,Ni zata yiwa wannan wulakacin saboda taga ina sonta ?

"wallahi sai na bar kasar nan, kuma a yau idan ba haka ba zan haukacemuku ,zan na tashi hankali kowa yau a gidan dan haka kusan yadda zan bar kasar nan .....
sai sai na ....ya kasa k'arasawa ya dunkule hannunsa ya bangon d'akin yana furzar da numfashi mai zafi ..
Sadik ya rungume shi ajikinsa "plz m.a kayi hakuri zamu San yadda za'ayi ka bar kasar but at least kasanyawa zuciyarka natsuwa.. numfashi kawai yake ja Yana saukewa tamkar mai cutar asma yana girgiza kai ..shi kawai yasan halin tashin hankali dayake ciki .

nabeel najin yadda sadik ke fama dashi gurin bashi hakuri amman yaki ,yasa ya d'auki wayarsa dake yashe da har lokacin ba'a katse Kiran ba ,cigabasa wayar ,inda yake tambayar "ko akwai jirgi mai zuwa nigeria ayau din ?
daga can bangaren aka bashi amsa da akwai amman sai gobe karfe shida zai tashi na safe.

"okay ka mana booking ya fad'a atakaice cikin tashi hankali ,sannan ya dawo ga bunayya ya tsura masa Ido Yana kallonsa ,duk ya wani firgice , gabad'aya ya rasa wani irin so bunayya yake wa muwaddat ,tun haduwarsu yasan da zaman muwaddat ,itace macen data hana mata dayawa samun gurbi acikin zuciyarsa ,duk macen daza tace tana son shi sai ya kusheta yace "muwaddat dinsa tafita kaza , ranar dai babu wanda ya runtsa acikinsu , Allah Allah suka dinga yi gari ya waye ya bar kasar..

Washegari tun asubar fari ya bar kasar london zuwa Nigeria ..

mmn sudais
2/10/20, 4:36 PM - imusamuhd(professor): Good
2/10/20, 4:38 PM - imusamuhd(professor): 💗💗💗💗💗💗
MUWADDAT
💖💖💖💖
💗💗💗💗💗💗

~NA~

AYSHA A BAGUDO

~DEDICATED TO~

AUNTY SALAMATU AYYUBA
(UMMIN KADUNA)

~BEST AUNTY FOREVER AND EVER~

warning!!!

" don't read this novel if you know you are not married... ❌❌❌coz this book contains only for mature people , if you read it, is for your own risk .....

WATTPAD @HAUESH

bismillahirrahmanirrahim

Wannan labarin na kudi ne idan kana /kina bukatar karantawa ki tuntu'bi wannan number 08059623096 or 08032384602

page 36

...Yana sauka a murtala international airport dake jahar Lagos ,bai tsaya kiran kowa ba, kai tsaye taxi ya d'auka zuwa fadeyi new side , yana zaune a bayan mota yana jijiga kafarsa d'aya had'e da cizan lip's dinsa na kasa , banda rawa babu abinda jikinsa yake,duk wanda ya gansa yasan akwai abinda ke damun zuciyarsa ,
sannan kallo d'aya zaka masa kasa cewar lallai an ta'bosa , sosai zuciyarsa ke bugawa da karfin gaske, ya kudurcewa ransa komai zai faru sai dai ya faru amman yau ko shi ko muwaddat acikin gidan ,
yaci alwashin sai shayar daita ruwan mamaki "ba dai shi tayiwa haka ba ,ya amince mata taci amanarsa ,ya yarda da ita fiyye da komai dake cikin duniyar nan, amman ta rasa da abinda zata saka masa dashi sai wasa da rayuwarsa, lallai yau za'ayi ruwan bala'i a gidan .....

wallahi sai ya tashi hankali kowa ,babu wanda zai bari ciki kuwa har da ummi abi da ita kan uwar gayya ....suna isowa bakin rafkeken get din gidan ya fito daga cikin motar a matukar firgice tamakar wani mahaukaci sabon kamu, tare da kamo duka lip's dinsa na kasa ya tura cikin bakinsa ..
cike da matsanancin tashin hankali ya nufi k'aramin get din gidan batare da ya tsaya ya sallami mai taxi din daya kawoshi ba ..

kai tsaye cikin part din ummi ya nufa ya shiga nemanta ,aikon yaci sa'ar ganinta a kitchen ta had'a zuma da madara cikin cup tana sha da spoon ahankali tana lumshe fararen idanunta .
juyowar nan da zata da niyyar fitowa taga cikin kitchen din taga mutun tsaye kikam tsaye abakin kofar ketchen , yana kallonta cikin tsananin tashin hankali da hargitsi.... tattare da tsagwaron 'bacin rai ,tamkar a mafarki take kallonsa ,dan hk ta murza idanunta da hannunta d'aya ta gani mafarki take, ko kuwa dai da gaske bunayya take kallo agabanta yana huci tamkar wani mayunwanci zaki .

Koda ta bud'e idanunta still shi din ta gani a tsaye agurin yana cigaba da kallonta cikin 'bacin rai kafin daga baya yasoma magana cikin d'aga murya da zafin zuciya yana nufo inda take " dole ki dinga min irin kallon mamaki mana saboda baki zaci ganina a daidai wannan lokacin ba ko...?

"Macuciya maciya amanar ruhi kawai.. "dan me zaki yarda ki auri wani ki barni bayan kinsa yadda nake tsananin kaunarki, da kaunar rayuwa dake ?

"ina can wata uwa duniya ina fama da tarin soyayyarki da tunanin yadda zan mallakeki arayuwata ,ke kuma kina nan ,kina had'a min zagon kasan kassara min rayuwata da neman yadda zaki kasheni ko?

Ya matso kusa daita sosai har suna iya jiyo bugun zuciyoyinsu, tare da kamo laulausar tafin hannuta cikin tafin hannunsa ya rike gam "me na miki muwaddat dana cancaci haka daga gareki?

"da kaunarki na rayu, na girma ina sonki kema kuma nasan kina mataanacin sona to me yasa zaki yiwa auwal dinki hk?

ya k'arasa maganar yana fisgota zuwa kijinsa ya kamkame ajikinsa cikin tashin hankali ,gabad'aya ya narke mata ajiki yana furta "why muwaddat why did you do this me?
"Bancanci haka agurinki ba, me ..me yasa zaki auri wani ki barni ya k'arasa maganar yana rabata da jikinsa yashiga jefa da duk abinda hannunsa yaci karo dashi acikin kitchen din yana ihu.... " kin ci amanata da amanar yarda dana miki.....
duk duniya babu macen da nake so nake jin dadinta fiyye dake amman shine zaki saka min da hakan .

da shaukinki na rayu ajkina, hka zalika kema nasan kina jin dadina fiyye da komai arayuwarki,me yasa zaki biyewa su ummi ki ci amanar kaunarmu ?

Cikin tashin hankali tashiga girgiza Masa Kai al'amun ba haka bane " wato ma yaudarata kike tun tsawon lokacin nan? ya kai hannunsa zai cafki wuyanta tayi saurin gocewa cikin firgici ta fito daga kitchen din a guje tana haki..

 ya biyo bayanta a zuciye yana k'ok'arin fixgota "ina zaki gudu kije ai wallahi sai dai kisan yadda zaki yi dani
 idan ba haka ba ,zan tada hankalin kowa a gidan nan,?
" zan addabi ruhin maciya amana a daidai bakin kofar d'akinta ya turketa yashiga zuba mata ruwan bala'I "zaki janyowa kanki maseefa muwaddat , wallahi sai na tarwatsa komai na wannan auren da za'a yi ,ke hatta al'ameen din zaki sa na salwarta da rayuwarsa "me kika d'auki ne ?
" shasha ...,mahaukaci da bai San abinda yake ba?
" a she yaudarar kaina nake dana yarda dake? jikinta da muryarta na rawa tace "kayiwa Allah kayi hakuri ,kayi shiru kar mutane sujika "

"an dade ba'a jini ba maciya amana kawai ,ai tunda har kika iya yarda zaki auri wani ki bani wallahi kowa sai yaji abinda ke tsakanimu dake ?

batasan sanda ta durkusa agabansa ba, hawaye na gangarowa bisa kuncinta "kayiwa Allah auwal karka min hk, karka tona asirinmu da wani ido zan dubi su ummi ?

"okay ni kuma wahalata ta tsawon shakara da shekaru ta tashi a banza kenan ?
"wallahi wallahi matukar baki bud'e baki kin fad'a musu cewar kin fasa wannan auren ba sai kowa yaji abinda ke tsakanimu har shi wannan tsinanen da zai auri saura na sai yasan komai ....

Take jikinta ya sake d'aukar rawa taji wani Abu ya gilma mata tun da ga tsakiyar kirjinta zuwa kasan mararta ,ta yi saurin runtse idanunta tana furta "ya Salam " hankalinta a matukar tashe take saurararon magangunsa hawaye na gangaro mata, can data rasa yadda zatayi dashi ga tashin hankali datake ciki ga ruwan balain dayake mata ,bata San sanda tayi magana cikin daka masa tsawa ba tace "To wai yanzu bunayya yaya kake son nayi da rayuwata ne ?
tana gama fad'ar hk tayi luuuuuuu ta yanke jiki zata fad'i adaidai lokacin ummi ta sanyo kai cikin parlour'n ,a matukar frigice yayi saurin tarota jikinsa ya rungumeta yana girgiza fuskatar "muwaddat ... aysha nah....aunty nah karki min haka na rokeki karki mutu ki barni.....
cak numfashin ummi ya tsaya ya daina aiki sakamako hango muwaddat dinta kwance bata numfashi.

wani irin razananniyar k'ara bunayya ya saki ya cici'beta bai tsaya wata wata ba sai waje,ummi tabi bayansa da kallo jikinta na kyarma "me zata gani yau?
"Me ke shirin faruwa agidanta ?

Inda motar ummi ke parke ya nufa daita yayinda direbanta bello dake k'ok'arin rufewa , yana hangoshi yayi saurin bud'e masa gidan bayan, bunayya ya sanyata a kujera baya ya k'araso ya fixge key'n mota a Hannu bello dake k'ok'arin shiga ya tayar , yashiga motar ya figa aguje .

Jin tashin mota yasa ummi dawowa cikin haiyacinta jikinta na rawa ta fito tana ihun kiran direbanta "bello ...!!!
aguje bello ya k'araso gareta dan daman yana tsaye ne yana mamakin abinda yasamu muwaddat.

A rud'e ummi tace juya kan mo....ai kafin ta k'arasa maganarta ya nufi wata motar cikin sauri, ya shiga yayi Mata key yana Jan motar baya , tashiga ta zauna jikinta na rawa kmr mazari, aguje suka bi bayan bunayya da gudu, yayinda ummi ke Kiran waya zuwa hospital dinta dan tasan can ya nufa.

tun kafin su k'araso tuni manya likitocin dake aiki a hospital din suna tsaye tsayuwar jiran karasowarsu sakamakon kiran gaugawa da suka samu daga shugaban asibitin ,atare motar bunayya data ummi suka k'araso ummi ta fito a gigice batare da ta tsaya rufe murfin kofar ba, jikinta na wani irin kyarma aka turo gadon d'aura marasa lafiya jikin motar da bunayya yazo daita , likitoci na k'ok'arin fito da muwaddat dake kwance tamkr matacciya, bunayya yaki yarda ,da kanshi ya cicci'bota ya d'aurata saman gadon marasa lafiya, aka shiga turawa cikin sauri sauri zuwa cikin hospital, inda ummi da bunayya ke biye dasu, ummi na bada umarnin ayi

office dinta da muwaddat ,shima bunayya na bada umarnin ayi nashi office din daita.

D'akin duba marasa lafiya aka samu nasarar shiga daita, likitoci suka shiga rawar jiki k'ok'arin dawo da numfashinta, har Allah ya taimaka ta sauke naunauyen ajiyar zuciya da atishawa sannan suka mata allurar bacci suka firfito.

bayan fitarsu ummi ta cigaba da kula daita ta zuki jininta domin gano abinda ke damunta, gwajin farko ummi ta tabbatar da muwaddat na d'auke da ciki , gabatan ne ya yanke ya bada wani irun rasssss.....

take kuma jikinta ya d'auki rawa, ta kuma k'ok'arin sake yi mata wani test din still dai the same result yake bayarwa ,bata yarda ba,ta saita computer domin yi mata scan, ana ta hango ciki kwance a mararta yana motsi ,kai kawai tashiga girgiza tana furta "impossible muwaddat dina kai ba dai ita ba ....

Cikin matsanancin tashin hankali ta zuki jinita ta fito daga d'akin da sauri,bunayya dake zariya a tsakankani d'akin yana gani fitowar ummin ya fada d'akin .

tana kwance idanunta a lumshe tana fidda numfashi ahankali, zuciyarta na bugawa da sauri sauri ,ya mugun tsareta da tsumammun idanunsa kafin ahankali ya yaye rigar da take sanye dashi sama, nan take idanunsa ya Kai kasan mararta inda zane dake gurin ya fito baro baro al'amun mai juna biyu ,runtse idanunsa yayi gabansa na fad'uwa ya kamo hannuta yana kallon farcenta, babu tantama ciki yake gani ajikinta Wanda yake da tabbacin nashi ne ,yayi saurin yin sama da rigar sosai zuwa inda brest dinta suka bayyana ,ya sake Kai idanunsa kasan mararta , tsagun dake kasan mararta ya fito rassss sai kyalli yake yi ,nonuwanta sun yi wani irin girma kmr an hurasu, ya zaro nononta d'aya daga cikin bra dinta ya tsurawa kan nipples dinta ido yana kallo yadda bakin yayi .....

kmr ya tashi ya gwadata domin sake tabbartawa yace "kai bazan bata lokacina a banza ba ...,duk alamomin dake jikinta sun rigada sun tabbatar masa da ciki gareta....

ahankali ya maida brest dinta cikin bra tare da sauke rigarta gumi na tsatsafo masa ,kafin kace me tuni kamaninsa ya sake sauyawa, ya k'ara wata rama, haka ya juya ya wuce yana kukan zuci ...

ummi kuwa wani babban hospital ta nufa tana kiran abi awaya yazo yasameta acan ,atare suka shiga hospital din yayi saurin k'arasowa inda take yana tambayarta "hubby meke faruwa ne? "jinin muwaddat na kawo a gwada min ...ta k'arasa mgnr tana kuka , "ke me yasa baza kiyi mata gwajin da kanki ba?
"muje kawai tayi gaba da sauri shima ya biyo bayanta hankalinsa a tashe yana gyara babbar rigarsa.

nan ma gwajin farko likitan yace juna biyu gareta ,wani irin kallo kallon ummi da abi sukewa

juna mai tattare da matsanancin tashin hankali.
"Kina jin abinda likita ya fad'a wai jinin muwaddat na d'auke da ciki ,"kai wannan ba gaskiya bane ,da al'amun wannan mahaukacin doctor ne, bai San aikinsa ba ,ai duk laifinki ne ta yaya kina babbar likita zaki kawo mutane wannan k'aramin hospital din dan kawai a 'batawa mutane moon dinsu ..
Baki ji yadda nake jin zuciyata ba a halin yanzu ,ina jin kamar ana zarar raina ne ,tashi tashi muje kiyi mata gwajin da kanki koma abar shi gabad'aya domin banga ta yadda za'a yi muwaddat tayi ciki ba ,sam wannan zance karya ne ba gaskiya ba ..
yana gama fad'a mata haka ya dubi likitan da yayi zaune rike da biro yana dubansa "likita kaje ka sauya sana'a zuwa kwasar shara,Dan shi ne ya kamaceka ba aikin likitanci ba, ya janyo hannu ummi cikin 'bacin rai suka fito tana goge hawaye saboda ita ta rigada ta yarda ta kuma amince ciki ne ga muwaddat dinta "
Abun tambaya wa yayi mata cikin ?

"Sannan a ina akayi shi?
shine abinda yake bata mamaki da d'aure mata kai daga asibitin nata asibinta suka nufa suka d'auko muwaddat wacce tun barin bunayya d'akin ta farka tana kuka.

Tun a mota jikinta yayi sanyi sakamakon ganin irin kukan da ummi take, tambayarta take son yi Amman ta kasa ,hk kawai take jin gabanta na fad'uwa har suka iso gida kuka ummi take shi dai abi bai ce mata komai ba saboda direban dake cikin motar..

A parlour'n gidan sukayi masauki gabadayansu inda suka iske bunayya zaune rike da wayarsa kallo daya yayi musu ya tabbatar da suna cikin tashin hankali fiyye da Wanda yake ciki ,ya d'auke idanunsa akansu saboda Sam iyayensa basu bashi tausayi ba, idan ma akwai Wanda zai tausayawa to muwaddat ce ,abi ne ya nunawa muwaddat gurin zama dan ta kasa samu natsuwar zama saboda irin kukan data ga ummi keyi ,ta zauna da kyar jikinta na rawa haka kirjinta na bugawa da karfin gaske sai lokacin tunanin ko bunayya ya fallasa sirrinsu ne yazo zuciyarta, tunda ta zauna ummi ke kallonta tana zubda hawaye abi yace "wai meye haka ne mukarama?

"wannan wani irin abu ne haka yarinyar nan nasan bata d'auke da komai ai kema cikakkiyar likita ce mai zaman kanta why not ki gwadata ki tabbatar da gaskiyar lamarin, ummi ta kalleshi da idanunta da suke cike da ruwan hawaye tace "gaskiya ne muwaddat na d'auke da ciki saboda ni na fara gwada da farko ,zuciyata taki yarda ,shiyasa kaji na kiraka mukaje gurin wannan likitan da nasan bazai fad'a min karya ba.

"What?
"How this thing happened?
Abi ya mike tsaye Yana kallon muwaddat a mugun atsorace "ciki muwaddat ?
"Ciki fa mukarama wani irin ciki gareta?
Ya juyo Yana sake duban muwaddat cike da tashin hankali ..

Yayinda take muwaddat ta fashe da kuka tana kallon bunayya dake zaune ya d'aura kafarsa d'aya bisa d'aya Yana karkad'awa "lallai idan ya tabbata ciki gareta to bunayya ne "Inna lillahi wa Inna lillahi raji'un"na shiga uku ni muwaddat ciki gareni ?
"To wazance yayi min ciki ?
Takarasa zance ciki wasu zafafan hawaye na wanke mata fuska ,Banda kalmar Inna lillahi wa Inna lillahi raji'un babu abinda muwaddat take furtawa acikin zuciyarta sannan ta d'aura hannuwanta duka saman kanta .

"Ba d'aura hannuwa saman Kai zaki yi ba , fad'a mana uban da yayi miki ciki zakiyi...
cikin wani irin yanayi na miskilanci yake kallonta batare da yayi tunani komai ba shi asalima dadi faruwar lamarin yayi , sai dai muwaddat ta bashi tausayi, yana jin kmr ya kamota jikinsa ya bata hakuri akan tashin hankali da take ciki .

Amman daya tuna abinda taso yi masa take yaji haushinta ya kamashi a ganinsa ma meye ya faru da har zata dinga irin wannan kukan tana dubansa , ahankali yake k'ara mata karfin gwaiwar amsa tambayar ummi ...

ummi banda kuka babu abinda take tana sake tambayarta Wanda yayi mata ciki amman muwaddat tayi shiru taki yin magana illa kukan datake ..
Shima abi gabad'aya mutuwar tsaye yayi ya dawo tamkar mutun mutumin har sai da ummi tace "abi kana jinmu kayi shiru kace wani abu mana," kace ta fad'a mana Wanda yayi mata Wannan cikin..

Abi ya kasa magana dan bazai iya ba ,kwata kwata bashi da wannan jarumtar ,ran ummi yayi matukar 'baci ganin tana neman 'bata musu lokaci ta mike tana k'ok'arin rufeta da duka abi ya riko hannunta "ka sake ni na yiwa wannan munafukar Allah dukan mutuwa ,maci amanar ruhi duk irin tarbiyar da muka baki wannana shine sakamakonmu ,"me zancewa yaya .....?

"Wani irin abun kunya ne wannan ?
"Muna d'aukarki salaha mun yarda dake mun amince miki a she zuwa kike kina yaudararmu ,kina cin amanarmu abayanmu ,ni ta ya ma kikayi acikin gidan nan baki fita koina ke kad'ai, baki zuwa islamiyya ....
makaranta ni ke kaiki da kaina, hatta direba ban yarda ya kai min ke koina ba ,ko malamin islamiyya yayi ciki .....

"kai ina wallahi bashi bane , tunda ga gurin karatunku can, ga mazaunina can ga naki ga na malam " a idanuna ake yin komai ... ta k'arasa mgnr tare da fashewa da wani kuka..

"ban rike amanar da aka bani ba ko?
ta fadi haka tana duban abi dake zaune ya girgiza mata kai ,sannan ya kamota ya mai daita Kan kujerar da ta tashi "ki samu natsuwa mukarama mu bita ahankali muji Wanda yayi mata , sannan ya numfasa ya Kira sunanta "muwaddat .....

ta d'ago kanta ahankali ta kalleshi tana kuka "waye yayi miki cikin jikinki ?

Bunayya dake zaune har lokacin rike da waya yace abi ummi ku daina wahalar da kanku cikina ne .....
gabadaya suka rud'e suka gigice suka ma rasa ta ina maganar ta fito atsakaninsu ,shi kuma bunayya da yayi maganar yayi kamar bashi ya fad'a ba, ya cigaba da latse latsen wayarsa hankalin kwance ..

mmn sudais